
# TAYAR DA ESTHERS NA ZAMANI

**LITTAFIN GLOBAL ADVANCE DOMIN HUKUNCIN KOYAR DA SHUGABANCI GA MATA**



CONNIE PARKER

**TA DA SU ESTA NA ZAMANIN NAN**
**LITTAFIN SHUGABANCI TA KUNGIYAR GLOBAL ADAVANCE**
**DON HORAS DA MATAYE**

Ba a yarda wani ya sake sayar da wannan
littafin ba sai dai kungiyar Global Adavance. An bada izini a sake buga darrusa
don horaswa, muddin za a rabar kyauta.

Sai da inda aka ambata, dukannin nasoshi daga sabon juyi aka dauka. Copyright © 2001 ta hannun crossway Bibles, hidimar wallafawa ta GoodNews.

© Connie M. Parker.

## ABINDA KE CIKI

**KALMAR FARKO……………………………………………………..…….4**

**GABATARWA………………………………………………………..……5**

NI WAYE

1. Shaida na a cikin Kristi…………………………………………...….7
2. Tafiya cikin Ruhu…………………………………………………...…15
3. Tsara Rayuwa ta……………………………………………………….20
4. Shawo kan abinda ya faru da ni a baya……………………………..27

DANGANTAKAN

5. Raya dangantakana da Allah………………………………………..34
6. Shugabanci ta bawa………………………………………………….45
7. Daraja, abin maida hankali, da kuma daida tawa…………………...52
8. Sadarwa, yanayin mutane, dangantaka……………………………..58

SHUGABANCINA

9. Yin shugabanci a inda Allah ya sanyaka……………………………67
10. Aikin hadin kai-shine mabudin shugabanci…………………………73
11. An kira don a bi………………………………………………………...79
12. Yin tunani yin buki kaddamarwa …………………………………...86

**KALMAR FARKO**

Ya Abokaina,

An kiraku ga babban manufa!

Wannan kungiya ta GLOBAL ADAVANCE ta baku wannan dauna ne domin ta gina bangaskiyarku ta kuma taimake ku domin ku shafi rauuka domin Kristi.

Yawan cin mutane da zasuyi anfani da wannan takarda suna rayuwa ne cikin an,adun do ake wulakanta mata . muna so ku san da cewa Allah yana tunani sosai akanku. Ya hallice ku cikin kamaninsa. Yana kaunar ku yana kuwa marmarin chanja rayuwanku. Kamar haka.Ba hatsari bane kiyi rayuwa a wannan lokachi na tarihi a wurin da Allah ya ajiye ki. Yanaso yayi amfani da ke domin ya tabi rayuwan wasu domin manufansa.

Addu'an mu shine ki sani kafafawa da izawa domin rinjayan sauran mataye hanya mai kyau. Kina da muhimanchi ga shirin Allah domin iyalinki da alumanki, da kasanki da duniya baki daya!

Kaddamarwa da farinciki

Jonathan Shibley Shugaba- Global Adavance whitney daughter, shugaban shiri.
ESTHER INITIATIVE

**GABATARWA**

18. sai yesu ya mastso yace musu, an mallaka mani dukan iro a sama da kasa 19. Don haka sai kuje ku almaji ranstadda dukan allumai, kuna yi musu baptisma da sunan uba da na da Ruhu mai tsarki, 20. Kuna roya musu su kiyaye duk iyakar abinda na umurane ku. Gashi ni kuma kullum ina tare daku har zuwa matutar zamani. Matta 28:18-20

Umarnan Yesu na karshe zuwa ga almaji ransa anan duniya, sune aininin zucciyan wannan takardan. Ko kun gane cewa ba wai kawai ya umurchi mabiyansa su jagaranchi mutane zuwa ceto da kuma yin masu alkawarin mulkin sama bane? An kuma umurche su da su da su " almajirantadda dukan allumai a kuma koya musu dukan abinda na umurnesu" wani babban kalubale. Domin "almajirantaswa" yana butatan mu mu bude rayuwa mu mukuma bada kanmu bada cicijewa ba domin jagorantan wasu zuwa ga kaunar juna, a kuma karfafa su nemi yin biyaya da dangantakarsu da manallichin duniya duka, maiceton rayukan mu ya zama mania bin farin ciki da kuna zarafi domin in rubuta wannan zakarda zuwa garetu in kuna bayana maku tafiya ta na shugabanchi. Wasu daga cikin darasosi da na koya tawurin lura ne da kuma gargadi daga manyan shugabani da na samu saduwa dasu, wasu kuma na karantane a litatafai ko kuma na saurara ne daga bito ko wa'azi na kuna sanya shi a aiki nanda nan, wasu kuma na koya ne daga nasara na da kuma fadiwana. Na kuma yarda cewa kaidodin tabbatatune huma basu rufe kan Magana da muke Magana a kai ba, amma na baku Karin kayayakin da zatu kara yin bincike idan wani kan Magana ya rikatar daku ko kuma na wani abu mussaman ko kuna yayi kama da abinda ke kike fuskanta.

Na rubuta wannnan darasi mussaman domin waddanda suke da mamarin kayayakin horaswan shugabanchi na litafi domin mata. Misalai da kuma dandanawa an samo ne daga hanga da mata suka yi. Idan ke mame ce cikin shugabanchi wanda ta mika kai domin gina tsara na gaba na shugabanni domin mulkin Allah, ina karfafa ki kiyi anfani da wannan darasi domin ya zama maki jagora na koyaswoyin shugabanchi goma shabiyu. Idan ke name ce wanda yanzu ne kike tara shugabanchin, cikin addui'a ki nemi wasu masu zuciya irin naki doimin samin wanda zata yarda ta rika anfani da hikimarta da kuma saninta domin koya miki.

Fata na shine kuyi binciken wannan darasin cikin alluma, wanda kowane mutuum yana karantawa yana binbini akan rayayakin kafin a fara taron ko a yanar gizo ko

ta ido da ido domin ayi tunani tare a kuna raba sani tare da kuma hikima domin karfafa juna.

Shugabanchi sani ne na kaskanchi. Idan baka tunanin kanta Kaman ajiyayen shugaba kana cikin tarin mutane masu kyau ba ina kamar Musa ko Gedion ko Dauda ba amma Allah ya zabesu domin su shugabanchi dubbai. Labari mai dadi shine ba Allah yana gaya mana mu almajirantadda wadanda zasu bi mu ba, amma almajirai wadanda  zamu jagotanta domin su bi yesu, shi wanda yake tare da mu a kullayaumi, wanda yake rike dukan iko a sama da kuma duniya.

Bari hikimarsa da kasancewarsa ya jagoranchi dukan mu yayin da muke bida mu bishi!.

## DARASI NA 1: SHAIDA NA A CIKIN KRISTI

Daya daga cikin kaidodin shugabanchi shine a bayyana wacece kaidodin shugabanchi shine a bayyana wacece ke da kuma inda zaki. Ba tare da wannan ba, da ke da masu bin ki akwai alamun tafiya barkatai ba wurin zuwa babu cimmo burin kome kamar masubi shaidannu cikin litafi sun bayyane. Nasossi daruruwa cikin litafi sun bayyana yadda Allah yace damu. Mune gishirin duniya, kuma hasken duniya, kama manzanin Kristi, kuma jikassa, aluma mai tsarki. Amma Allah yana ce dani haifuwa na biyu (Yohana 3:3). Wanman ya chanja shaidana? Idan haka, ta yaya? In kama ba haka ba to ta yaya? Bulus ya bayyana amsoshin wadannan tanbayoyi; da karfi a cikin afisawa, wasikan da ya rubuta ma “tsarkaka masu aminchi cikin Kristi yesu “wanda ya kunshi har da mu.

1. Ni mai albarka ne; “yabo ya tabbata ga Allah ubangiji mu yesu almasihu da dansa kuma wada yayi mana albarka da kowace albarka ta ruhu, basamaniya a cikin Almasihu “(Afisawa 1:3) wannan Kalman “Albarka” Kalmar helenenci, wanda maananta shine, yin Magana mai kyau akan wani. Ina albarkatan (Magana mai kyau akan Allah) wanda ya albarkachi (Magana mai kyau a kaina). Ina kwatanchi dadin da mutum zai ji idan Allah wanda da ikon maganarsa duniya ta kasanche doga rashin komi, ya furta kowane albarkan ruhaniya a raina cikin Kriati? Duk sa’anda na sami raunana ko kuma cikin damuwa ganin bani da wani abnu da zan bayar, yakan yi Magana mai kyau akai ma, yakan yabe ni, yakuma albarkacheni

da dukan albarkan ruhaniya. Cikin tsonon alkawari, iyaye sukan furta albarka bisa yayausa ka tuna do Yakubu da ya albarkachi jikokinsa a masar, sai kuma albarkan Dauda a bisan Solomon? Akwai bayananen iko cikin albarka, sa'anan Allah ubanmu ya kuma hada mu da kowane albarkan ruhaniya yi tunani akan abinda wannan yake nufi.

2. Ni zababbe ne "Domin kuwa ya zababe mu a cikin Almasihu tun ba a hallici duniya ba, mu zama tsarkaka, marasa aibu a gabansa." (Afisawa 1:4). Allah ne da kansa ya zabe ni ko da menene wani yake tunani ko kuma yake cewa, ni ban zama Kurkure bane ko kuma kasan cewa ns ya zama hatsari. Ko da iyaye na basu ji dadin zamana mace Ba, Allah ya zabeni in zama mache, mache wanda Allah yana ji dani. Kasancewa na bai zama a kuraren lokachi ba. Allah ya zabeni kafin kafutan duniya ya mulmula ni a cikin uwata (zabura 139:13) Kalmar helenanchi na zabe ekiegomai ma'anar, "ki zaba ma kanki". Ya zabe ni yak kuna maida ni kamar nasa. A kasuwa inda mukan yi zabenyayan itatuwa, mukan zaba mafi kyau, kuma mai tsabta, ba domin yadda yake ba, amma domin amfanin da muke gani a cikinsa kuma da muhinnin dalili a zuciya domin wannan. Kada zabe da Allah yayi mana ya zama sanadiyar fahariya garemu domin Allah yakan zabi mara a zanchi da kuma rauana a idanun duniya ( 1 korintiyawa 1:27). Amma zai iza mu da bege da karfafawa ya kai mu bisa guwawamu yayinda mun gane cewa muna jingine dashi ne; … (2 korintiyawa 12:9)
3. Ya kaunache ni; "… cikin kauna ya kaddara mu zama yayansa" (Afisawa 1:4-5). Daruruwan nasossi da ayoyi sun kwatanta zurfin kaunar Allah mara karewa ga yayansa, amma wanda yafi na Romawa 8:38-39 da Romawa 5:7-8.
   38. Domin na tabbata ko mutuwa ce, ko rai, ko malaiku, ko manyan malaiku, ko alamuran yanzu, ko alamura masu zuwa, ko masu iko, 39. Ko tsawo, ko zurfi, kai, kowace irin hallita ma, ba zasu iya raba mu da kaunar da Allah yake yi mana ta wurin Almasihu yesu ubangijimu ba
   7. Da kyar za a sami wanda zai bada ransa saboda mutum mai adalchi, ko dayake watakila saboda mutun mai nagarta wani ma sai yayi ka sai da ransa 8. Amma kuwa Allah yana tabbatar mana da kaunar da yake yi mana, wato tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu domin mu."

Mai yiwuwa wasumu bazasu san tsananin kuanan iyayemu na duniya ba, kuma kaunar Allah zai iyo zama musu kamar mafarkin abinda ba zai yiwu ba, amma kuma can cikin zukartan mu muna marmarinta, wato kaunar da ke da karf, kaunar da babu kashedi, kaunar mai juyayi, da kirki da bayaswa hannu sake, da gafartawa da kuma natsuwa. Yana bada har fiye da wannan. Wasumu mai yiwuwa sun fuskanchi wani mummuna bakin ciki suna tambaya cewa, "Idan Allah yana kauna da iko don me ya bari wannan abin ya faru dani? Yana so musani cewa a tsakiyan zafi, yana nan a wurin, kuma zuciyansa tana zafi tare da namu. Yana marabtanmu idan muka gudu zuwa wurinsa. Wasu kamar ni zamu san kauna da kuma alherin uba mai kirki. Ya zama mani da sauki in gaskanta da hikima da gafaran ubanmu na sama. Na dube shi kamar ubana wanda nassa bautan gumaka. Amma kana bazan manta ranan da ina kwance cikin rashin lafiya da Allah yayi Magana dani cewa, "Inaso in zama babanka." A saanan ne nag ani kamar wani abu ya fodo daga idanu na, sai nan da nan ya zama inda zan sami taimako? Karfi da inuwan zama da kuma gaskiya. Ban juya bay aba. Idan kana marmarin sani cewa Allah uba yana kaunarka da kuana mara iyaka, ka roke shi ya bayana maka wannan gaskiya a zurciyarta saanan ka fara nemansa a wuraren da baka sa tsammani zaka sameshi ba a rayuwanka.

4. An saye ni "Ya kaddara mu mu zama yayansa tawurin yesu Almasihu bias ga nufinsa" (Afisawa 1:5) Ba wai Allah ya zabeni kawai ba, ya kuma albarkachechi ba, ya kuma kaunace nib a, amma ya saye ni zuwa cikin iyalinssa ya bani gado. Yohana 1:12, Afisawa 1:11, Galatiyawa

NOTES

4:6-7 Wannan babban zarafi ne kasancewa a iyalin Allah, in sadu da dukan yanuwana a duniya duka. Ba lalle mu zama yare daya ko aladu daya ba, amma ubanmu daya ne mai cetomu daya do kuma ruhu daya wanda ya hada mu cikin kauna da kuna kulo da juna.

5. An karbeni: “Domin mu yabi daukakar alherinsa kaunatachensa.” (Afisawa 1:6) Wanna kalma “karba” Kalmar helenanchi ne “charitoo" wanda yana nufin “a iske yana da kyau da kuma banshaawa” A wani kayadadden lokachi da akayi anfani da Kalmar helenanchi a sabon alkawari shine a cikin luka 1:28 da malaika ya gaida maryamu kamar mai saman tagomashi ubangaji  ya iske ni da farin ciki cikin kaunatattu. Ya dauki jin dodi akaina. Ya karbeni yace na sami tagomashi sosai. Mata suna kauna mu saurrari labarum juna mu kuma tattauna akansu. Dangantaka yana da muhinmanchi a garemu kauna mata, yans kara mana karfi yana kumsa ingiza ruhumu. Yin kyauna abu ne mai wuyan yi a garemu, ciwon yakan yi zurfi sosai. Abin mamaki ne mu san da cewa sarkin sarakuna yana kaunar mu ya kuma karbemu yadda muke. Ba zai yashemu ko ya boye mana ba. Ya gaya mana muzo gareshe gabagadi zuwa kursiyinsa (Ibraniyawa 4:16). Da nayi addu’a sai nayi hoton dakin zinariya mai kyau da Allah zaune a bisa an daukaka shi. Yayin da na kusanchi kofan sai fuskansa ta haskata da jin dadi sai ya marabcheni ba zuwa wurinsa ba kadai kamar mai rokon tagomashi, amma sai ya bude hannunsa domin in gudu zuwa wurin ubana, ya kana karbeni. “ya karbeni” “ya bani tagomoshi” kana abin “jin dadinsa.”

6. An fansheni; “Ta garshe ne muka sami fansa albarkachi jinisa.” (Afisawa 1:7) Kalmar fansa a helenanchi shine “apolytrosis” tushen maanan Kalman ita ce “kwatanta yadda ake sakin wadanda ke a kurkuku, bude abubuwanda ke aa rufe, yana kuna rushe Katanga. A cikin litafin rutu an bayana hoton yadda fansa take A kwanakin rutu, idan iyali suna cikin tabarbarewa, sai wani dangi na kusa da iyalin ya dauki nawayan iyalin. (a halin da ita Rutu ta shiga) Dole yayi fansa domin rayuwan iyalin da kuma kayansu wanda sun shiga cikin dauri. (Kittei,1964 p.330.) Da fadiwan Adamu a gonan aidin, an sayar da mu ga dauri ga zunubi, mun zama bayi ga zunubi (1 Korintiyawa 15:22, Romawa 6:16-22) Amma Allah tawurin jinin yesu biya kudin fansa domin ya bamu yanchi daga zunubi da ya kawas da bangon kurkuku na zunubi da ya sa mu a daure. Ya maida mu ga iyalinsa (Romawa 6:8) Labarin Rutu labarin   mu ne. Yesu, shine boaz namu,




sarkimu da mai fansanmu, ya biya tamanin fansar mu domin mayar da dangantakar mu da uban mu wanda ke cikin sama.

7. An gafarta mani: … wato yafewar laifofinmu bisa ga yalwar alherin Allah. Afisawa 1:7b An yafe mani abinda nayi a baya. Dukansu! Na zama mai tsarki da kuma adalchi a idanun Allah "…. Allah ya suturache ta da ceto da nasara ya rufeni da rigan aldachi. (Ishaya 61:10) Na "Dauki sabon halin nan da aka halita bisa ga kamanin Allah da hakikanin adalchi da tsarki (Afisawa 4:24) kamar Ibrahim, "Na gaskanta Allah, bangaskiyan nan tasa kum aka lisafta ta adalchi ce a gareshi" (Romawa 4:3). Zan iya ganewa da dauda saanda yace, "mai farinciki ne mutumin da aka gafarta masa zunubansa, maifarinciki kuma wanda aka gafarta masa laifofinsa 2. Maifarin ciki ne wanda ubangiji bai zarge shi akan wani laifi ba, wanda ba algus ko kadan a cikinsa (Zabura 32:1-2). Maanar "kurakurai" a harshe helenanchi "pesa" tana nufin zunubin tayaswa" (nasan bashi da kyau amma na cigaba da aikata shi hakanan) har irin wadannan zunubai ma Allah yana gafartawa. Dauda ma ya fuskanchi hakanan zai sani. Allah ya kuma gafarta mini sauran zunubai na da na aikata da kuma kurakurai da dukan mugun tunanin zuciyana. Hukunchin zunubi na yesu ya biya da jinisa, kuma ina da tsabbachi cewa idan na furta zunubai na shi mai aminchi ne da zai yafe mini zunubai nay a kuma wanke ni daga dukan rashin adalchi. (1Yohana 1:9). Babu wani abinda zanyi in sami gafara." Gama tawurin alheri aka ceceku tawurin

bangaskiya. Wannnan ba yin ki bane, amma kyautan Allah ne, ba sakaumakan aiki bane, domin kada kowa yayi tunkaho (Afisawa 2: 8-9)

8. Ina zaune tare dashi a sammai: "A cikin Almasihu yesu kuma ya tashe mu tare, har ya bamu wurin zama tare a samaniya." (Afisawa 2:6) Lokachin da yake a gaban manyan firistoci yesu ya bada wannan shaida, cewa doga yanzu dan mutun zai zauna a hannun daman a ikon Allah" (luka 22:69) Yesu ya san inda zashi, sai ya dauke mu tare dashi. Menene hatsarin wannan? A cikin Kristi mun sami iko bisa magabchi. Muna da nawaya muyi anfani da wannan iko a chikin sunan yesu.
9. An kirani: "A kuma sa ku ku waye ta idon zuci, domin ku san ko menene began nan da ya kiraku a kai da kuma ko menene yalwar gadonsa mai daukaka a game da tsarkaka" (Afisawa 1:18) Ya kirani domin inyi rayuwa da bege!!

## AYAR HADDECEWA

- 1 YOHANA 3:2 "Ya ku kaunatattu na a yanzu mu yayan Allah ne yadda zamu zama nan gaba kuwa, ba a bayan aba takuna, amma mun sani saada ya bayana zamu zama karmasa domin zamu ganshi kamar yadda yake."
- Afisawa 1:3-6 "3. Yabo ya tabbata ga Allahmu ubangijimu Yesu almasihu, da ubansa kuma wanda yayi mana albarka da kdwace albarka ta ruhu, basamaniya. A ccikin Almasihu tun ba a hallichi duniya ba, mu zama tsarkaka, marasa aibu a gabansa. 5. Ya kaddara mu mu zama yayansa tawurin yesu Almasihu, bisa ga nufinsa na alheri. 6. Domin mu yabi daukakar alherisa wanda ya bamu kyauta hannu sake saboda kaunatachensa."

## MABUDIN GASKIYA

Na sami albarka. An zabeni, An kaunache ni, An maid ani dan gida, An karbeni. An tanshe ni. An gafarta mani. Na zauna tare dashi a madaukaatan sammai. An kirani.

## MARTANIN KA

1. Cikin wadannan bayanan gaskiya dauka zayyana a sama, ki zabi guda uku wadanda sun zama maki da muhinmachi sosai. Yaya ganewan wadannan bayanan gaskiyan zai iya chanja hanyan da kike tunani akanki, da kuma yadda kike tunani akan Allah da kuma yadda kike tunani akan mutane da kin kula dasu a rayuwanki?

a.________________________________________________________

b.________________________________________________________

c.________________________________________________________

2. Cikin wadannan gaskiya wanne ne yafi zama maki da wuya ki gaskanta? Wani mataki ne zaki dauka gobe domin ya kara maki karbuwa na wannan gaskiyan game da kanki? Mai sauki ne tawurin yin addu'a a kullun domin Allah ya bayyanan ya kuma tabbatar da wannan gaskiyan ga zuciyanki ko kuma gaskiya tsarki kallafa kanki wajen binciken litafi mai tsarki akan abimda Allah ya fada akanshi ko kuma wasu matakai da Allah ya sanya a zuciyan ki.
3. Wanne ne cikin bayana gaskiyan nan yafi maki sasuki karba kuma dom me kike tunanin haka ne? akwai lokachi da wani aya a nassi ko abinciken litafi ko ganewa na kanki ko wahayi doga wurin Allah ko kuma wani abu daban ya tabbatar da wannan gaskiyar a zuciyanki!

## DOMIN BINNCIKE NA GABA


Yana kauna na – wayne Jacobsen (Jacobsen 2000)
Gaskanta da Allah – Beth Moore (Moore 2004)
Albarka – Smalley da Trent (Smalley & Trent 1986)

**KOYASWA NA 2: TAFIYA CIKIN RUHU**

**SABON NI: JIKI, RAI, DA RUHU**

Allah ys hallice mu da wadannan martabai guda uku, amma kuma bangarori masu daukaka Ruhu, rai, da jiki (1 Tasalonikawa 5:23) Idan muna tunanin rai kamar shine zuciyanmu nufimu da tunanin mu, saanan ruhumu ya zama kamar mu din kenan, ga hanya mai sauki da zama dubi wannan hoton.

Saanda na zama maibi, Ruhuna ne ya s ani na zama sabo (2 korintawa 5:17)




JInikaa ya tsaya a yadda yake, ba kiba ko ranewa ko chanjin caunin fatan jiki saanan raina (Zuciyata,nufina, da kuma ji na) su ma ba a chanjasu ba. Idan dama can ni ban iya lissafi ba kafin in zama maibi. Haka din ba zai chanja bayan na zama maibi idan ina da kakkauran raayi kafin in zama maibi, ko bayan na zama maibi naka din zan cigaba da zama. Idan ina fama da ciwon zuciya kafin in zama maibi, ko bayan na zama maibi ina haka zai cigaba da zama. Menene ya zama sabo? Ruhuna!! Da na sami ceto, Allah ya sanya kayan sadarwa a cikina – a ruhuna – Romawa 8:14 yace kamar dan Allah, Ruhun Allah ne

zai bi dani. Yana wannan zai faru? Ruhunsa yana saduwa da Ruhuna akai da sasssautan murya (1 sarakuna 19:11-12). Amma koda RUHUna yana so ya bi abinda Allah ya gaya mani inyi, zuciyana da nufina daji na da jikina basu bar matsayinsu na bishewa ba tare da wani gwagwarmaya ba.

## SABONTA ZUCHIYA NA

Tilas ne in fara yin yadda zan chanja zuciyata, (Romawa 12:2) tawurin karanta da binciken maganan Allah,saanan tawurin addu'a kino binciken littafi da kuma gane halayensa da kuma manufafinsa. Zan kuma karfafa Ruhuna tayi girma da karfi tawurin addu'a, da wakkoki cikin Ruhu, da kuma addu'a cikin Ruhu (Yahuda 20) Yau inda Ruhuna ke girma, ina kara samun karfi bis raina (Zuciya, da nufi da ji) da jikina. Saanda maganan Allah yana sabonta rayuwa na, hakana kuma zai fara sabawa da ayukan Ruhun Allah (Yohanna 15:3)

Amma kuma labari mai dadi da kuma mara dadi shine zuciyata tana sabontuwa da abinda nike ciyar dashi idan na ciyar dashi da maganar Allah, zai sabontu ta wurin maganar Allah. Idan kuma na cigaba da ciyar dashi ababa mara kyau kamar kallon fiina fiinai mara kyau ko karatun litattafai da basu da kyau da kuma wasu maganganun banza da sauran wasu ababa mara kyau, sabonta irin wannan zuciya yana daukan lokachi.

Biye da abinda yake jagorantan duk abinda ke shiga zuciyata, dole ne in ba Ruhuna dama domin ya mallake ni Philibiyawa 4:8, yace, " ko menene yake na gaskiya ko, menene abin girmamawa, komenene daidai, ko menene tsatsarka, ko menene abin kauna, ko menene daddadar Magana, in ina da wani abu mafifichi ko abin da ya chanchanci yabo, akan wadannan abubuwa zakuyi tunani." Amma kuma abin takalchi, sa'anda munyi mumunan Magana sai wannan ya kaimu ga cikata mumnan aiki (misalai 23:7)

Karmar uwa matashiya da kananar yara masu tasowa guda biyu, nasha fama a wannan fannin. Ba tare da lamirin tunani ba, yayin da nike chanja masu kayan fisari ko kuma nike share musu majina a hanchi sai in iske kaina ina wani tunani daban akan mutane da alamu ransua rayuwana.

Sai inyi mamakin yadda tunani na ya kai wajen da sauri haka. Wata rana sai ina tunanin ganin kaina na makale karkashi wani kogo, sai nayi tunanin yin addu'a nace, Ubangiji idan dai kawai zaka sa ni in gane mumunan tunani saanda nike a bias tudu zai fi zama mini da sauki in dauna gangarawa kosai" sai na fara soma


kowane rana da wannan addu'an sai Allah wannan ganewa cikin Ruhuna." Kada kaje na fara haddace nasossi ko raira wakokin sujada ko kuma sauraron wakokin da zasu tayar da ruhuna zuwa inda yake da tsarki da kuma kauna."

Ba mu bukatan mu kashe kanmu saanda muka iska kuma cikin mugun tunani amma muna bukatan mu tuba. Mugun tunani zunubi ne domin yana gaba da maganar Allah (Filibiyawa 4:8) ka roki Ruhu mai tsarki ya rinjaye ka a duk saanda ka fara mugun tunani (Yohana 16:7-8) kada ki yi kokarin yin nasara da yakokin rayuwa da kanki yana nan domin ya taiimake ki. Ki roke shi ya taimake ki domin  ki cigaba. Ki fara rike Filibiyawa 1:6 wannda yace," Na tabbata shi wanda ya fara  kyakyawan aiki a gareku, zai karasa shi, har ya zuwa ranar yesu Almasihu" Zan iya koya yadda zan sannu halaya mai kyau a rayuwata.

**MIKA NUFINA DA JI NA**

Ba wai zuciyana ne kadai za a chanja ba, amma kuma dole in koya ina nufina yadda zata mika kanta ga ruhun Allah. Bulus ya sa shi kamar "an giciyeni tare da Kristi yanzu ba nine nike rayuwa kuma ba, ama Kristi wanda ke cikina. Saanda rayuwa da nike yi ayanza a cikin jiki ina yi ne da bangaskiya cikin dan Allah, wanda ya kaunacheni ya bada ransa dimin na (Galatiyawa 2:20) A kullum dole ne in "giciye" nufina domin in fara zaben hanyan Allah. Wannnan domin maida shi uban gijine a kowanne gefe na rayuwata, har da tunani na. ji na ma dole zai fara yadda da Ruhun Allah wanda shine yake zaune koya yadda zamu iya kawas da ciwon zuciya na baya, amma a yanzu zamu dubi wani tambaya mai sauki da sabon maibi yakan yi. Na sani ya kamata inji "dadi" ko yaushe (Filibiyawa 4:4, 1 Tassalonikawa 5:6) na kuma karanta game da masubi da suka yi rayuwa a wannnan hanya amma yaya zan koya yin wannan?

NOTES




Afisawa 5:20 yana dauke da wannan asirin “kullum ku rike gode wa Allah uba da sunan uban gijinu yesu Almasihu akan ko mene ne.”

Wani mutun mai suna corrite ten Boom ya bada labarin yadda ya koyi gode ma Allah domin wasu kwari a inda suke zaman buya a wani sansani a lokachi yakin duniya na biyu, saanda yar uwanta ta tuna mata yadda wadannan kwari suka kori yan tsaroo yayinda zan koya niyi rayuwa da zuciyan godiiya ta gaskiya in kuma yi godiya domin kalubale mai tsanani a rayuwa na, ina furta murna da zurfaan salama a ruhuna. Ina bada gaskiya ga Allah da alamurana, da sanin cewa yayi alkawari yin kome da kyau, ko wanda zan ga mai kyau din yanzu ko kuma wani lokachi (Romawa 8:28). Yayinda abubuwa suna tafiya ba yadda ake so ba, kuma nayi iyakan abinda zan iya yi, sai in zaba in bada gaskiya cewa Allah yana da wani wani shiri daban inda shirinsa domin zai fito. Daganan zan bar komai a hannun Allah maimakon yin kokarin chanja shirin da kaina, ina mika nufina zuwa gareshi. Sai nazo ga gamewa cewa muddin na ba murna da salama doma domin su cika Ruhuna, hakanan zan cigana da walawa cikin ruhun Allah zan kuma kara samun begen abubuwa masu kyau ko a cikin yanayi mafi wuya. Wannnan begen ne ibraniyawa 6:19 ya saya mana cewa “karma anko yake ga rai kafaffe, tabbatache.” A cikin duniya mai cike da rudani ta tashin hankali ina bukata anka a rayuwata. Duk da haka dai ubangiji yana jira yayi muku alheri. A shirye  yake yayi muku jinkai, domin a kullum yana aikata abinda yake daidai. Ta wurin dogara ga ubangiji ake samun farin cikki.

**AYYAR HADDACEWA:**

- 11 Korintiyawa 5;17 Saboda haka duk wanda yake na Almasihu sabuwar hallinta ne, tsohon alamari duk ya shude, gashi kome ya zama sabo."
- Yahuda 20 – Amma ya ku kalmatattuna, ku rika inganta kanku ga bangaskiyarku mafi tsarki, kuna addu'a da ikon Ruhu mai tsarki."
- Romawa 12:2 kada ku biye wa zamanin nan amma ku bar halinku ya sake, tawurin sabunta hankalinku dugum, don ku tabbatar da abinda Allah yake so, wato nufinsa kyakyawa abin karba cikkake kuma.
- Galatiyawa 5:16 maganata ita ce kuyi zaman Ruhu, ba kwa zaku biye wa halin mutuntaka ba."

**MABUDIN GASKIYA:**

Tafiya tare da Allah yana bukatan horas da jiki a kullum, sabonta zuciya da warkar da ji na zuciya da kuma mikawa. Akwai kalubalantarwa da hukuntarwa, amma a bayyane yana yantaswa, yana haskakawa yana kuma bada rai, domin ba an kafata da nufina mutuntaka bane, amma tawurin amsa rayuwan Ruhaniya ta yau da kullum.

**MARTANIN KI:**

1. Wane bangaronin rayuwanki (jiki, zuciya, da nufi da kuma ji) ne kike yawan samum kalubale da yake hana Ruhu mai tsarki ya bishe ki? Ki dauki lokachi kina tunani da kuma addu'a akan
2. Wane mataki ne zaki dauka gobe domin yin karanin nasara a bangarenki?

**DOMIN BINCIKE NA GABA:**

Tasabtache taron bita- masu hidiman tsabtache Rafi. (Hidimomin 1999)

Hali mai nasara- john Maxwell, (Maxwell, 1993)

Dagan yaki na zuciya- joyce myer (meyer,1995)



**DARASI NA 3: TSARA RAYUWATA**


Dukan shekaruna na hidima,, na saurari labaru da dama akan yayan Allah. Kamalawa na bai zama samadiyar rahoton binciken kimiyya ba, na iya na lura da abubuwa guda uku:

1. Saanda mata da dama sun taso ne daga gidan da iyayen basu zuwa ikkisiya, yawancin wandannan matayen sun gane, ko cikin mamakinsu cewa kamar kananan yara akan sa sus a yi addu'a su gaskanta da Allah.
2. A kalla rabi daga cikin matan da sun bani labatinsu sun zama  wadanda sun fuskanchi fyade ne kamar yara. Yawancin su basu yi wannnan zanchen da wani ba, amma kama sai suka gani yafi sauki suyi Magana a asirce.
3. Akwai iko, hikima karfafawa da karfi cikin Magana, da kuma ji, da binbini akan darashin da aka koya daga labarum mu.

Wannan darasi tananan domin ta jagoranche ku tawurin tunani akan tafiya ta ruhaniya ." niyyaan shine tawurin addu'a aani wai wane ga abubuwan da suka gudana a rayuwanka  domin ya baki sabon tunani akan ke wacece da kuna yodda Allah yake shiryaki yana kuna sarrafa ki domin abinda yake kiranki kiyi a cikin tafiyanki na shugabanchi.

**GADONA:**

Ki shirya itachhen iyali da sunayen da kuma dangantakar yanuwa da suka shafi rayuwanki a hanya mai kyau. Kada ki hada da ranana haifuwa ko na mutuwa




wadanda baki sani ba, munufan ba wai ana so a suke kirkiro wani zuciya bane amma domin sanin wadanda sun shafi rayuwanki a hanya mai kyau. A karkahin kowane suna ki sa yadda kike dashi da kuna abinda yayi da ya shafi rayuwanki.

Ga misali kamar haka:

Mary Ann Munday: Mamana

- Ta koya mini farin cikin bautan wasu
- Ta bayyana kaskanchi yadda zanyi nasara da abokin gaba.

Mai yiwuwa akwai kakaninka wadanda ba ka san su ba, amma sun yi wani kudiri mai kyau wanda yake shafanki yanzu. Mai yiwuwa sunyi kudiri su zama masu zuwa kasasshe ko su fara sanaar da zai chanja rayuwwan iyalinsu.

Wannan cikin Allah a rayuwaki shine gadonki, ko da yake abin ya faru kafin ma a haife ki.

**LABARIN RAYUWATA:**

Kiyi tunani akan rayuwaki shekkaru biyar nana baya zuwa yanzu. A wata yar takarda ko a takardan rubutu, a kowance shekaru biyar ka rubutar wani abu mafi muhimanchi da ya fari da kai a rayuwan ka, da kuma mutanen da sun shafi rayuwan ka da kuma wu raren da ka lafi. Ki kara da wasu kalamai kadan na daillin da yasa suna da muhimanchi.

Kiyi tunani akan:

1. Masu wuya – musammam yanayi mai zafi ko mutane ko kuma sani
2. Jin dadi – samun farinciki mai girma da kuma wadar zuci.

3. Masu iza ki – mutanen da suke karfafaki da masu renonki da iyayenki da kuma abokanki na kusa, da shugabani da zaka samu da kuma mutane da kin kasanta labarinsu.
4. Allah cikin aiki – Abubuwan da kin gaskanta dasu “Hannun Allah” ne a rayuwanki

Misali: Daga Haifuwa zuwa shekaru biyar:

MUTANE:

1. Uwa
2. Uba
3. Yaruwa
4. Danuwa

WURARE

1. Gida
2. Gidan kakanni
3. Ikklisiya


AYYUKA:

1. Haifuwan danuwa ko yaruwa
2. Fara makaranta
3. Motsawan iyali

ABINDA AKA FI SON YI:

1. Taimakon mamana a kawayen gida
2. Nishantar da baki
3. Taimakon malami na a aji.

Kayi wannan a kowane Karin shekaru 5 na rayuwanka. Daga shekara 6 - 10, da kuma shekaru 11 -15 da sauransu.




1. Da wannan bayanin kiyi anfani da wannan layin ki kwatanata alamura da kin fuskanta a rayuwanki ko mai kyau ko mara kyau. Za ki iay kara tsawon layin inda bukatan hakna ki kara kalma daya ko biyu domin kwatanka ayyuka mutun ko wuri wanda zai rinjayi tunaninki. Idan zaki shirya wannan hoton ki rubuta lambobi daga 1 -12 bisa ga shekaru bisa tunaninki, da ruhaniya da kuma mataki na alamura a wannan shekaru.
2. Sai ki kara jan wani layi ta wani launi domin kwatanta matsaloli masu kyau da marasa kyau na rayuwanki a kowane lokachi.
3. Kiyi amfani da layi na uku a wani launi daban kuma domin kwatanta matsaloli masu kyau da marasa kyau na ruhaniya (tadiyanki da Allah.)

**KIRANA BAIWA NA DA JUYAYINA**

Yayinda kike tunani akan gadonki da kuma labarin rayuwanki ki zabi ayyuka guda uku ko wani yanayi wanda kina ji kina nan a wurin da Allah yakeso ki kosance, kino kuma yin abinda aka hallice ki kiyi. Yana iya yiwuwa wani takainanen abu ne. ko kuma mai yuwuwa lokachi ne wanda kin dukufa wajin ayyukan da suke kalubalantan ki amma duk da hakanan kin iya kin alwatar dashi da kyau. Kiyi anfani da wannan wurin da aka bari domin ki kwatanta kowane daya daga cikin labarin ki a takaiche da bayani a fili yadda kin iya tunawa. Yayinda kina rubuta wa, sai ki amsa wadannan tambayoyi:

Yaya zan fara aiwatar da wannan?

a. Me nayi?

b. Yaya zan gama shi?
c. Yaya zan san cewa nayi shi daidai?
d. Me nafi so game da shi?

Labari na 1:

Labarin na 2:

Labarin na 3:

A wannan karon ki gaya ma abokiyanki da kika yarda da ita, ki gaya mata duka yadda kina iya tunawa, kina gaya maata abinda kinyi ki kalli kanki kina aaikata wannan abin ki kumakwatanta yadda kin sami kwanciyar rai a wannan yanayi. Aikin abokiyanki shine ta saurareki tana rubuta wasu abubuwa da kin gaya mata da kuma yadda kin gansu shin kwantar maki  da rai, saanan da wani kafa gane da inda kike ko kuma wanda kike tare da ita. Saanan dake da abokiyanki zaku duba labarin duka ku gwada inda suka yi kama da juna.

**A TAKAICHE**

Idan kina nan ke kadai, sai kiyi tunani akan abin da ya sameki abaya sai ki roki Allah ya baki hanga cikin abinda kika koya akanki ko kuma kiransa da kuma manufansa akan wannan kiran. Menene kike juyayi akanshi yan zu? Wani baiwa ne kike dashi wanda zai zama da amfani cikin hidima a wannan gefan? Wasu bayebayen suna iya zama baa yin wasu abab da har yanzu baki san maanarsu ba, amma kuna sai ki rika ganin cewa “labarin bai cika ba”, shine manufan Allah bai bayyana ba tukuna. Kalmar ni kaina, yayin da ina wannan aiki, na gane cewa ina da juyayi ga “mata da sana’a”. Ba da bata lokachi ba nayi murabus daga aikina kamar darekta na maaikan mata, saanan a shekara 65 na cusa kaina ga Karin karatu

ta fannin harkokin kasuwanchi a wata makaranta da take koyar da tauhidi da kasuwanchi. Abinda kin sani zai iya kuwo maki chanji a rayuwa amma kada ki yi shakkan aikin Allah don zai iya shiga Tsakani domin ya jagoranchi hanyoyinki zuwa nasa.

**AYAR HADDECEWA**

- Zabura 139:12-16; 13. Kaine ka hallichi kowace gaba ta jikina, kaine ka harhada ni a cikin mahaifi yata. 14. Ina yabonka gama kai abin tsoro ne dukan abinda ka yi sabo da ne, mai ban mamaki. 15. Ka ga lokachi da kasusuwa ne suke sihatuwa saadda kuno ake harhadas su a jhankali a cikin mahalfiyata lokavchin da nake girma a asirche. 16. Ka ganni kafin a haifeni. Ka kididdige kwanakin da ka kaddara mini duk an rubutaa su a litafinka, tun kafin faruwar kowanensu.
- Zabura 37:23-24; 23. Ubangiji yakan bi da mutuum lafiya a hanyar da ya kamata yabi yakan ji dadin halinsa, 24. In ya fadi ba zai yi war war ba, gama ubangiji zai taimakeshi ya tashi tsaye!!

**MABUDIN GASKIYA:**

Allah yana tare da ke tun cikin cikin mahaifiyarki, a lokachi hargitsi da kuma lokachin farin ciki, ko kana sane da kasancewarsa ko baka sane, babu abinda zai rabaka da kaunarsa.

**MARTANINKI:**

1. Wadanne bayebaye ne kike tunani kina da shi wanda Allah ya baki, amma har yanzu yana nan ba anfani, ba ki sarrafa shi domin mulkinsa ba?
2. Wane mataki za ku iya ɗauka a yanzu ko cikin shekaru 5 masu zuwa “gano” wannan kyautar, don kawo ta saman inda zai iya kasancewa da ci gaba?

## DOMIN KARIN BINCIKE:

Menene baiwanki? (Hendricks, 2013)

Gane baiwanki (Bock, 2015)

Masu neman karfi 2.0 Tom Ruth (Rath 2014)

Baiwanki na ruhu maitsarki – Peter wagner – (wagner, 1994)

Gane baiwan da Allah ya baki – Don &Katle Fortune. (Fortune & Fortune, 1987)

Sharhin baiwan ruhu mai tsarki kyauta (Gibert, 2015).



## DARASI NA 4: SHAWO KAN ABINDA YA FARU DANI A BAYA

Yanzu da kin dauki lokachi kina tunani akan gadonki da kuma rayuwanki, lokachine yanzu da zaki yi tunani akan wadannan mutane, ko wurare ko ayyuka su cigaba da tsara maki rayuwanki, da dangantakarki da kuma hidimar ki. Hikima da hanga da kuma albarku da wasu zuka zubo maki yana zubowa tawurin ki kuma Kina albarkachi wasu. Yaya mugun yanayi da wahala ya shafi dangantakarki? Babu mamaki wasu daga cikinsu sun sa  ki  kin zama da Karin juyayi da kuma mai shawara da kula da kuma aboki (2Timoti 2:2)

Ke kadai ce zaki iya kammalawa ko abinda kin fuskanta a baya mai “kyau ne mai saci ne!! Tambayan ita ce menene zaki yi domin ki fadada abu mai kyau saanan ki rage abu mara kyau da ya shafe ki a baya domin gyara a shekaru masu zuwa.

## TUNA BAYA AKAN NASARORI

Ki dauki yan mintochi kiyi tunani akan ababan jin dadi a rayuwanki, lokatai da kike ji kamar kina yin abinda Allah ya halliche ki kiyi kuma kin ga hannun albarkansa. Menene kike tunani? Ko kina Faharinya akan abinda kin iya kin aiwatar? Ko kuma tunanin komawa zuwa wurin? Ko alaman bakinciki ko tsoron cewa kwanakin daukakar ki zasu wuce saanan kome zai tabarbare daga nan? Menene darasin da zamu koya daga nasa roorin mu? Akwai su da dama da suka zo zuuciyata. Allah zai iya bayyana maka wasu da sun shafeka kai kadai, amma ga kadan da yo koya mini.

## DARASI NA 4: SHAWO KAN ABINDA YA FARU DANI A BAYA

Saanda nayi aiki tukuru na sami nasarori da dama abu ne mai yawiwa mutun ya shiga ruhun fahariya. Mai yuwiwa tawurin hikima ban yi fahariya game da nasarori na ba a gabanmutane, amma murna? Fahariya rami ne mai hatsari ga shugabanni. Babu inda muke samun wannnan darasin fiye da labarin sarki Nebuchadnezzar, wanda bayan ya iske kanshi ya isa, sai aka gargade shi tawurin wahayi, saanan kaskanchi mai tsanani ta sameshi. Kaji gargadin sa. “Wadanda suke tafiya cikin fahariya shi zai kaskantadda su. (Daniel 4:30-37) Akwai lokachi da mukan gane aikin Allah cikin samun nasaran mu da damanda alajibi takan bude ko ta rufe, ko kuma muryan ruhu mai tsarki duke bi da mu zuwa kudiri mai wuya da kuma saduwa ta Allahintaka. Amma idan muka yi aiki tukuru hat muka cimma burimu mutane dake kawaye damu suna taya murnan samun nasara, yana da sauki mu manta da wanda ya bamu idanun gani da kunnuwa naji, da kwakwaiwa don tunani da kuma zarafofin uimi domin koyo, da kuma kaumatattun iyayaenmu wadanda suka rernemu tun daga jariai. Yakan kuma zama da sauki muhi tunani cewa munyi nasara ne ta wurin kokarin kanmu, sai mu kasa gode masa do kuna wadanda suka taimakamu yin wannan nasaran. Yayin da kike tunani akan jin dadinki, kin una godiya ga Allah. Idan kuna baki erigaya kin yi haka bas ai ki yi tunanin rubuta wanin dan takarda na waya ga wadanda suka sa rayuwanki ta yi dabam.

Idan kina damuwa ko kina tsoron cewa abu mafi kyau ya wuce.” Zabura 139:16 yace, Allah ya rubuta a cikin takardansa, “ka kididdige kwanakin da ka kaddara mini, tun kafin faruwar kowannesu.” Muddin kina nun fasawa, Allah yana da aikinda yana so kiyi masa domin faddada mulkinsa. Tambayan it ace ko zaki iya kawas da idanuki daga abinda ya rigaya ya wuce da dadewa ki fuskanchi wanayi nag aba. Mai waazi A.R Bernarel cikin sanannen waazinsa da yace, “Wahallinka gabatanka” ya ayi gargadi cewa, mutunin da bashi da wahayi mutuum ne da bashi da gabata saanan mutumin da bashi da gabata a koyaushe yakan koma cikin gabata ya rigaya ya wuce. Bitrus ya jagoranchi sauran almajirai zuwa kamun kifi bayan mutuwan Yesu, naomi mata koma kasarta israila bayan mutuwan maigidanta da yaranta, Adamu shima da ya koma gonan aidin idan da Allah bai hanashi yin hakaba idan kin iske kanaki kina zakiyi makanki shine, ko kin rasa ruya nag aba wanda Allah ya shirya maki (Irmiya 29:11)

### WARKARDA CIWON ZUCIYA

Dukan mu dai munt aba fuskanata wani yanayi a rayuwan mu wanda mukw ganin kamar duniyan tazo karshe a wajance. Misali idan muka rasa wani kaunatachen mu, ko kuma likita ya gano wani ciwo agaramu, ko rasa aiki, ko tabarbarewar kudi,

ko kuma tawayen yara, ko cin amanan abokai, ko rarrabuwar dangantaka, ko kuma dai duk wani abu da kin dauka kamar abinda yake kara maki mamuyachin lokachi adarasi n abaya. Giwon zuciya da mun samu a lokachi wannan mawuyachin lokachi yakan rataya a zurfafan ruhunmu na shekaru, bayan nan sai ya sake bullowa da zafi, a lokachinda bane tunanin zuwansa, sai ya sake tayar da ciwon zuciya na fushi da tsoro da kiyayya da yashewa da musgunawa da firgichi da kunya da kashewa ko kuma wasu ji da sun shafi kudirin mu da kuma dangantakar na yanzu.

Tambayan it ace idan bamu karbi warkaswan ciwon zuciya nana da nan a lokachi samun ceto ba, yaya zamu sane shi? Zai ma yiwu kuwa?


Bari in tabbartar maku, Yesu shine mai warkaswa, ban a jiki kawai ba, har ma da na azaban zuciyas. Shine mai gyara karyayen zuciya. Zai iya warkada wadannan cututuka tawurin alajibi nan da nan, ko kuma atsananke kamar yadda ake bare albasa daga bari daya zuwa bari daya. Daga sanina akwai layuka dayawa tsakanin ciwon jiki da ciwon zuciya bukata. Ciwon dake bayyane a jinkin mutuum baya bukatan kula da mayar do hankali do kuma bada lokachi kamar wanda yake a maran mutun mayan anyi mashi aiki. Za a iya samun wannan da sauki wajen shafa masa mai da kuma daura masa bandeji, ko kuma bashi dan lokachi hakanan ciwon zuciya, mugayen kalamai da husunan, sakamakon su yak an zama harbi ne nan da na,amma tantache magan dawuri, da Kalman neman gafara da kuma tabbachin kauna da bangrima shine ansa mafi dachewa. Nan da nan akan samu warware maganan da kuma saukin  mantawa misalai 19:11 ya bada shawara cewa "mutuum mai hankali yaka danne fushinsa. Lokachin da wani ya cuce ka, abin kirko ne kayi kaunan baka kula dashi ba,"

Amma babanciwo mai zurfi bashi da saukin yin magani, cin amana aboki mafi kusa, da kuma rudin mai bada shawara da kin yarda da ita da kuma tarzoman da cin kasa sansantawa wanda yakan jawo kalamai masu zafi ko rashin aldachi. Wandannan suna bukatan mayar da hankali. Idan aka barshi hakanan, wannan ciwon zuciya yakan fadodo ne saanda muka cigaba da tunanin laifin da akayi mana abaya batare da yin addu'a domin sansantawa ba ko kuma kin bada dama do dachin zuciya ya kafu a zuciyanki (Ibraniyawa 12:15) mukan dauka cewa tawurin nuna muna son gaskiya da adalchi ne kawai yayi nasara amma can cikin zukatanmu akwai ciwo mai zubadda guba a zukantamu da dangantakarmu. Sai tawurin gafartawa na gaske ake samun warkaswa da yanci. Nassin a bayyane take. Gafartawa ba zaqbi bane gam ai bi. Cikin matta 6:15 yesu yace, "in kuwa baku

yafe wa mutane laifofinsu ba, ubanku ma ba zai yafe muku naku ba." Gafarkuwa ba yana nufin cewa abinda mutun yayi maki ba zafi cewa ko kuma wannan yo ba mutuum dama ya sake aikata laifin ba. Kuma gafartawa ba lalle ne sai mun sake dawo da dangantaka dake tsakanin mu da mutumin ba. Idan sun kasa gare laifin da sunyi har sun neman su sake kuwa mana hari, sai mu sake gafartawa, amma a wannan karan kayi kaunan daga nesa. Gafartawan namu ne, don haka guban rashin gafara ba zai lalata dangantakmu ya saba mana. Yaya zamu iya sani idan da gaske mun yafe abinda aka yi mana? Idan wannan abinda aka yi mana baya shafan kudirimu na yanzu zamu san cewa mun samu yanchi daga ikonta abisanmu. Ki tuna cewa gafartawa abinda ya kemata ya cigaba ne a kullum ba sau daya ba kawai duk saanda aka saba maki, ki zaba ki yi gafara. Akwai kuma tuyata mai zurfi na mara mai kana da ciwon zuciya wanda yakan zo a sanadiyar tsoro ko kuma tarzoman da mutun ya fuskanta ko a matsayin wanda abin ya shafa ko kamar shaida. Har yanzu shine mai gyara zukata da kuma mai warkasuwa. Babu wani yanayi da yafi kaarfin tabawarsa. Kamar yadda ciwo zuciya muna ganinsa hakanan ma ciwo zuciya yana da zurfi sosai harma ana iya ganinsa a waje kamar yankakken dangantaka da kuma kuntsarren fuska da magangamu masu dachi, da tsoro da rashin tsaro da yake hana girma. Kamar yadda yake a ciwo da yake a waje yesu yana warkass da ciwon zuciya daga ciki zuwa waje.

Yaya zamu iya sani ko muna da ciwon zuciya a baya wanda yana bukatan aiki a gefenmu domin samun yanci? Yawancin mu mun fuskanchi lokatai Idan wani yace ko kuma yayi sai mu iske kamu muna maida martini a hanayan da ko mu din ma, a lokachi zafin mu sai mu gaane cewa zafin ya wuce misali: me ya kawo wannan? Sau da dama yakan zama wani ciwon zuciya

NOTES




ne wanda shaifan yana anfani dashi kaamr tarko domin ya kuma mu da mugun tunani sau da dama karya ne da mukan zo ga ganewa a lokachi mai wuya. Sai karyan nan ta rikemu a zukatanmu har sai gaskiyan ta yantas damu (Yohana 8:32)

Wani mataki zamu dauka domin samu warkawan ciwon zuciya da kuma samun yanchi?

Kasa san cewa: (zaka iya nema wani balagaggen aboki mai ruhaniya wanda zai kasance tare da kai yayi addu'a tare da kai yayinda kake bin wadannan matakai)

1. Kazo gaban ubanka na sama a natse ka sansance bukatunka don taimako da kuma warkaswa.
2. Ka roki Ruhu mai tsarki ya taimake ka ka gane menene makasuddin ciwonka. Zai iya kawo maka abinda ya wuce cikin tunanin ka, ko kuma muryan ruhunsa yayi Magana da zuciyanka. Zakayi mamaki abin zaka karba, amma ka bada gaskiya ga shugabancinsa
3. Ka roke shin in akwai wani abu da yake so ka sani game da wannan yanayi saanan ya bayyana maka karairayi da ka bada gaskiya garesu a sakamakon wannan.
4. Ki tuba ki roki Allah ya gafarta maki. Yarda da karyan shaitan zunubi ne. mai yiwuwa akwai wasu zunubai da kika aikata da suke hade da wannan yanayin shina . kamar shiga cikin kungiyan asiri zunubi ne, da kuma hada rai da masu halayen shaye shayee zzunubi ne.
5. Ki roki Allah in akwai wanda kike bukatan gafaratwan ta, saanan kiyi biyaya da abin da ta gaya maki. Rike rashin gafara a zuciya zunubi ne. kada ki manta kiyi ma Allah godiya domin gafarnsa da ikon warkaswansa.

Idan mawuyancin lokachi suna kalubalatan mu. Saanan kuma tana da illa a rayuwanmu, don me Allah mai kauna ba zai tsare mu daga wannan zafi da kuma gwagwamanya ba? wasu zasu bada shaida cewa irin wannan lokachi ne muke girma da karfi ina ma ache mun bi nufinsa mun jingina a gareshi sosai har karshe.

**AYAR HADDACEWA**

- Yohana 8:32 – "Zaku san gaskiya, gaskiyar kuwa zata yanta ku."
- 2korintiyawa 10:4-5- 4. Don kuwa makamammu na fama ba na mutuntakan bane, naikon Allah ne, masu rushe makamai masu karfi. 5. Muna ka da masu hujojji a cikin zace – zancensu, muna rushe kowace ganuwar alfarma mai tare sanin Allah, muna kuma jan hankali kowa ga bautar almasihu."
- 1korintiyawa 10:13 – "bawani gwajin da ya taba samunku, wanda a saba yi wa dan adan ba. Allah mai alkawari ne, ba zai kuwa yarda a gwada kun fin karfinku ba, amma a game da gwajin sai ya bada mafita, yadda zaku iya jure shi."

**MUBUDIN GASKIYA**

Son Allah shine mu sani yanchi daga daurin mu na baya, mu dube ta maimakon haka tawurin gaskiyansa, gafaran zunubi tsabatachen lamiri warkakkun ciwo nasara da shaitan, nasara a bisan tsoro, da kuma mayar da kauna.

**MARTANIIN KI:**

Idan kika iske kanki kina yawan neman gafara a wurin Allah a kowane gafe na rayuwanki, ki samu lokachi a kadaiche tare dashi ki roke shi ya nuna maki, dalilin a yasa kin kasa samun nasara a bisa wannan matsakan. A gareni zunubin fahariya ne wata rana da na furta shi, amma duk da haka, sai naji ubangiji yace" kinaso ki kawas da wannan? "Da gaske tunanin bai zo mani da cewa zan sani yanchi ba. martini na nan da nan shine "I" cikin mintochi goma sha biyar nayi tunanin abubuwa da dama da nayi gasa da wasu, (yau uwana, abokaina da mijina) sai na sami fahariya wajen "nasara." Saanan ya nuna mani yadda wannan ruhun gasa ya shafi dangantakan na har ya kai ga ruhun kishi wanda ya samu tushe a cikin zuciyata. Wannan ita ta zama mafarin tafiyata ta yanchi. Menene Allah yake yayi maki Magana akai?

## DOMIN BINCHIKE NA GABA:


Chikakken yanchi- Robert Morris (Morris 2005)

Gafara da mantawa – Lewis Smedes (Smedes 1984)

**DARASI NA 5: RAYA DANNGANTAKANA DA ALLAH**

Kamar yadda muke bukatan motsa jikin mu domin mu kiyaye lafiyan jikimu hakanan ne muke bukatan mu motsa ruhaniyan mu domin mu tabbatar da lafiyan ruhaniyan mu. Wannan sura ta kunshi yanayin motsa ruhaniyan mu har guda goma sha biyu (12) a takaiche wanda take da anfani domin wannan manufa. Ba zaki yi anfani da dukansu a kullum ba, ko kuma a kowane yanayi na rayuwanki ba, amma ki san da cewa akwai su kuma masu bi da dama sunyi anfani dasu har shekaaru da dama. Yesu da kansa ma ya kara inganta su yayinda yake a duniya. Idan ki koya ki gwada wannan horaswa zasu taimakeki kiyi girma a ruhaniya ki kuma samu dangantaka mai zurfi da Allah.zasu kuma taimakeki ki zama da sani da kuma kansancewa a ruhaniya da yake kawo irin wannnan tunani daban da na yanayin jiki da mukan so da hankalin mu. Labari mai dadi shine bamu bukatan mu zama masu ilimin tauhidi sosai kafin mu iya samun irin wannanhoraswa zuciya mai marmarin Allah (zabura 42:1-2) yin addini ko kuma duba ruhaniyanki ba shine burinmu. Burin shine mu iya kawas da zunubinmu da kuma son zuciyan mu. Idan mum yikokarin fuskantan wadannan da ikon kanmu farisawa, wadanda sunyi kokari yin anfani da abubuwan dake a bayyane domin su maganche abubuwa na zuciya. Zai zama a bayyane cewa mun kasa. Gama daga cikin zuciya baki yakan yi Magana "(Matta 12:34). Allah ne kadai yake chanja zuciya amma wannan horaswan zai taimakemu mu shirya zukatamu ga Allah domin yin aikinsa.

Cikin misalin mashuki. Yesu yace iri shine Kalmar Allah, saanan kasa shine zuciya. Zuciya tunani akan wannan horaswan kamar gyara kasan zuciyarki domin




iri na maganar Allah ya sami saiwoyi yayi girma (galatiyawa 6:8, luka 8:5-8). Yanzu kina nan a tsarke tawurin Kalmar Allah da nayi maki (Yohana 15:3).

## SASHI NA DAYA: TARBIYYAR RUHU

### 1. SUJADA

Yesu ya gaya wa wannan matan a baakin rijiya cewa Allah yana neman wadannda zasu bauta masa cikin Ruhu da kuma gaskiya (Yohana 4:23). Menene wannan yake nufi? Yi tunani akan wannan na kankanin lokachi. A gareni yana nufi yana neman wadanda zasu zu gabansa cikinkauna da kaskanchi, gaskiya da budadden zuciya ba tareda yin riya ba ko kuma wani boyayyen zunubi ko wani abu daban da ba a bayyana ba, kin a bashi girman da ya kamache shi. Bugu da kari Zabura 95:6 ta gaya mana muyi sujada mu rusuna kasa, bari mu durkusa a gaban ubangiji mahallincimu. Ko kuma a durkushe a guwawun mu ko babu, saanda munyi ma ubangiji sujada zukatanmu zasu zama cikin Allah halin kaskanchi da kuma martaba shi. Ya kamata muyi masa sujada cikin tsarkinsa a karkashin sawunsa da hannaye masu tsabta da zuciya mai tsarki. (zabura 29:2, 99:5, 24:4)

Bada kanmu ga sujada da yabo abinda Allah yak enema kenan, ba wai yana da wani abu da yake kara masa ba, amma domin abinda yake yi a cikinmu. Yayinda muka sansanche daukakarsa da ikonsa, da girmansa, damuwoyimmu da kuna lokachi alamuran mu zasu dauki hankalinsa.

Sujada na iya daukan sslo da dama kamar sauraron wakokin sujada wanda yakan zaunadda ruhun mu shiru, ko hada hannu da na gana daya ko waka cikin ruhu, to addu'a cikin ruhu, ko durkusawa, ko kwantawa rub da ciiki, ko tada hannayen mu sama wajen mika kai ga Allah, ko dai duk abinda kin iya yi cikin ruhu domin zuwa gabansa yanayin mu na jiki bashi da muhinmachi

fiye da ruhunmu ya sami hadi da ruhunsa cikin kauna, daraja da martaba. Kizo gaban sa da halin sauraro, a shirye ki bada duka yadda kike a gareshi.

2. **FURCHIN TUBA**

Cibiyar gaskiya na bishara ita ce yesu yam utu domin zunubanmu. Ya dauki hukunchi da mune ya kamatamu dauka, domin mu samu gafara, da wankewa da kuma rai madawami.

Cikin 1Yohana 1:9, mun karanta cewa "In kuwa muka bayyana zunubanmu to shim ai alkawari ne, mai adalchi kuma, zai kuwa gafara mana zunuban mu, ya tsarkake mu daga dukan rashin adalchi."

Gaskiyan shin ko bayan mun samu sake haifuwa zunubi yana munne damu, kuma a kullum mukan aikaata muna kuma tunanin abubuwan da suke bata ma Ruhu mai tsarki rai. Mukan sami raunana mu fuskanchi wadannan zunubai da adalinsu, muna kuma sane da raunana mu sai mu sake karban alherin Allah. Idan muan so muyi girma ta ruhaniya ba zamu shugabanci rayuwan da ba a bincikawa ba.

A koyaushe ka zama kana rokon Allah domin ya bayyana maka mussaman abubuwanda kayi tunaninnsu ko ka fodesu ko kuma ka cikato su wanda sun bata masa zuciya, saaanan ki sauran amsansa. "jarraba ni ya Allah kasan tunani na gwada ni ka gane damuwata. Kabincike ko akwai wani rashin gaskiya a gareni. Kabi dani a madawwaniyar hanya" (Zabura 139:23-24)

Hade da zunubin zuciya (kamar fahariya tsoro kyashi da kuma fushi) zunubi jiki (kamar rogonnchi zina) abubuwanda kin aikata da kuma abinda ya kamata da kinyi amma ba kiyi sub a, ko baki fode sub a, baki kuma ji shi ba, baki kuma yi tunanin su baaa.

Yayinda Ruhu mai tsarki yake bayyana maki abubuwa, ki tuba kin ema gafaratawansa. Ki karbi warkaswansa da shafewansa sai ki tuna ki kamalla wannan furchinki da kalmomin Zabura 51:1o- "ka hallita tsarkakakiyar zuciya a cikina ya Allah kasa sabon halin biyaya a cikina."

Ki zama mai neman sulhuntawa da Allah a kullayayomi. Duk innda ruhu mai tsarki ya kashe ki akan zunubi, ki tuba nan da nan ki nnemi gafartawan sa. Ba lalle ne sake bincika rayuwanki akan hanya ko kuma ki rusundda kanki ba. sai dai Ruhunki ne ya sami hadi da Ruhunssa. Ki tuna yana kaunaki yana kuma da marmarin yin zumuta dake akai akai. Yana kauna baki ganewa na kasancewarsa da salama. 1timota 5:17

3. **ADDU'A**

idan yasan kome yana koina, don me muke addu'a? cikin addu'a mukan kulla dangantaka mai karfi da uba. Yin addu'a shine chanji muddin muna zuwa kurkusa da Allah da tsarkinsa, hakanan zamu gani bukatan mu na chanji, da kuma bada kamu ga Kristi. Sai mu fara tunanin irin na muka saurari amsoshinsa, zamuji muryarsa idan baki da tabbachi ko kanajin shi ko babu sai kit amban kauki ko abinda kike ji yayi dai dai da abinda Allah ya bayyana kansa agareki cikin kalmarsa. Mukan gane murya aboki a waya domin mun saba jin muryarsa a koyashe. Idan wani ya fadi wani abu akan aboki mai kyau mun san hallin abokinmu zamu kana iya sani in abinda am fada akanta daidai ne. hakanan tawurin maimaki ne mukan ji mu kuma gane murya Allah. Addu'a hanya biyu ne na sadarwa. Tumakin Allah suna jin muryarsa. Zai yi Magana dake (Yohana 10:27)

addu'a wani abu ne da zamu koya daga wurin YEsu, ko daga wurin abokai da sun koya yin affu'a da gaske, ko daga litafi mai tsarki (Halayan litafi da gargadi na litafi) ko daga litattafai akan addu'a da kuma aikata su. Addu'a yana kawa banbanchi (Yakub 5:16, I korintiyawa 3:9). Kiyi addu'a domin mara lafiya, da addu'a domin aure da kuma addu'a domin gwamnati domin patochi da masu bishara da iyalai da abokai domin karya, har ma domin baki iyakan wadanda Allah ya nuna maki su.

**HANYOYI UKU DA SUN KAMATA ABI DOMIN ADDU'A**

DABARA TA 1: Addu'a ubangiji- kiyi binbini akan yanayin addu'an maimakon sabawa da kalmomin.

DABARA TA 2: Grimamawa furchin tuba da godiya da kuma mikawa (ga wasu0

DABARA TA 3: Addu'a, Tuba, Roko, sa rai, da kuma karba

4. **NAZARI**

Nazari yana nufin binbini ko tagumi idan kin san yadda zaki damu, dole zaki san yadda zakiyi tunani?

Akan mr zakiyi tunani? Nassin ta gayarmana muyi tunani akan magan Allah, da sharunsa, da kaunarsa, da ayyukansa, da kuma alkawaransa, da alajinansa. (Joshua 1;8, zabura 48:9, 77:12, 119:27, 48, 143:5)

Yaya kike tunani? Ki fara da shirya lokachi da kuma wuri domin kada a dameki. Nikan yi wannan da safe idan ina tafiya. Wasu kuma sukan zauna shiru alolokinsu ko kuma suna bincike. Ki roki Allah ya nuna maki gaskiyarsa a zurciyanki. Idan allamura suna damunki, ki roki Allah mai

yuwuwa akwai abinda yakeso ki sani ko kiyi akan alamarin. Yayin da kike addu'a domin wasu, tsakan a madadinsu. Ki saurari muryan Ruhu mai tsarki maimakon yin kokarrin yin kome da kanki.

Wani sakamako ne ki ke sa ran zaki samu daga tunai? Bias ga nassi, zaki sa ran samunn tuba, da biyayya. Da hikima, da kuma ganin sabobin halaye cikin Allah, da kaunarsa tsrakinsa da kuma ikonsa (zabura 119:97, 101-102) kiyi hakuri da kanki yayinda kin koya wannan horaswan idan ya zama sabo ne a gareki.

**SASHI NA 2: HORAS DA RAI (ZUCIYA, NUFI, TUNANI ZUKATA)**

5. **BINCHIKE**

Binchike ta kunshi sharhi akan maganan Allah domin ya sabonta zuciya ya kuma tona shi ga gaskiya (Romawa 12:2, filibiyawa 4:8). Ba kanar tunani wanda take bukata kiuyi anfani da abinda Allah yake Magana dake a zuciya ba, binchike dukan nassi ne domin a gane abinda ke bayyane akan Allah, da hallayansa, da manufansa da kuma kaidodi a rayuwa. "Domin a iya rarrabe Kalmar gaskiya" yana bukatan bada hankali, da sharhi da kuma hikima na ruhu maitsarki kayayyakuin binchike suna nan da yawa a hanan alaka da sauran nasossi da kuma ganewarki na halayan Allah da kuma manufansa? Babu wani yanke cikin binchike zai dauki lokachi da kuma horas da kai kini Magana da wani da saninsa da hikimansata ruhaniya kike martaba domin ki fara. Kamus mai kyau na litafin binchike domin farawa da kyau. Idan kina iya shiga yanar gizo akwai kafafe da yawa da suke da kayan bincike a kyauta. Akwai kadan daga cikinsu a rubuce a karshen wannan babi.

Ki fara kowane bincike da addu'a ki kuma roki ruhu mai tsaki ya baki hikima da ganewa. Wata dabaran itace ki karanta ayoyi da yawa na nassi kai tsaye domin ya kwantadda tunaninki da kuma jin ki.saanan ki karatan kananan nasossi a natse sai ki dubi wuraren da suka boda domin Karin bincike litafi mai tsarki. Ki zayyana wasu ayoyi a litafinki, ki kumar ja layi mussaman wadanda sun zama da karuwa a gareki akan abinda kika koya. Idan akwai abinda kin karanta da baki gane ba ko kuma yayi kuma da wani abu da kim yarda dashi ya zama da gaske, ki roki Allah ya baki hikima Yakubu 1:5, sai ki tuntubi masu sharhi ko kamus da sauran wasu kayayaki domin ganin abinda wasu suka gano. Kiyi Magana da wanda ya ballaga a ruhaniya kin kuma yarda dashi, amma kuma kiyi lura da wani sabon koyaswa. Ku zanta akan raayoyin ku da junanku domin ganin ko sunyi daidai da sauran nasossi.

6. **KADAICHI**

   Kadaichi shine zama shiru ba tare da neman wanda zai yi Magana dake ba. Wani lokavchi sai mu saba da surutu wanda shine yakan kawas da kadaichi ya kasa bamu kwanciyan hankali.

   Sau da dama Yesu yakan fice daga taruwan jama'a har ma daga almajiransa domin ya bidi fuskan ubansa ya kuma ji muryansa. (matta 4:1-11, luka 6:12, matta 14:13, 23, markus 1:35, 6:31, lukaa 5:16). Zama a kadaiche bazai sa muji kadaichi ba. Zamu koyi jin dadin lokachin shiru na "lokachi kadaichi" da ubanmu ko da sassafe kafin ki tashi daga gado, ko kuma ab una karshe da dare kafin ki kwanta barchi, ko lokachin da kike a layi a moto, ko kuma kwanakin shiru cikin jeji.yayin da muke shiru da zukatan mu a gabansa ba da wani shiri ba ko kuma tunanin wani zanche da ya wuche ba. Zai yi maganan karfafawa ga zukatanmu, ya kuma bamu ganewa game da abubuwan da suna damun mu (Ishaya 30:15)

   Yayinda muke koyon halin kadaichi zamu samu karfi da salama a cikinmu. Wadar zuci da murna zasu kara ma hankalin mu tunani akan bukatan wasu da juyayi akan zafinsu.

7. **MIKA KAI**

   Mika kai shine yanci daga masu mallakanmu zuwa zaman kashin kanmu. Ba yana maida raayinmu mara muhinmachi bane, amma zabi ne muyi musum nufinmu mubi Yesu, da bada gaskiya cewa hanyarsa zai kawo farchiki mai grima da kuma cika alkawari Maarkus 8:34-35. Mika kai hali ne da kuma aiki.

   Yesu ya bamu missali, yana rayueansa da mika kansa ga unbansa,ko da zai rasa ranssa ne (Filibiyawa 2:4-7, Yohana 5:30, 8:28, matta 26:39). Bai rayuwa da mika kai ga farisawa ko kuma ga raayin mutane ba (markus 12:14). Ko dayake yayi ryuwa a karkashin gwamnatin Romawa (markus 12:16)

   A ikklisiya na farko an gargadi bayi su zaba suyi biyaya da iyayen gidansu, ko da su iyayen gidan suna musgana musu (Bitrus 2:18-21) ko dayake basu da wani zabi. Kamar masu bi, Bitrus yana gaya musu cewa suna da zabi sai su zabi su mika kai ga wandanda suke da iko a bisa kansu. Bulus ya shawarci mataye su mika kai ga mazajensu kamar  ga ubangiji (Afisawa 5:22-24). Bitus ya gargadi masu karatansa su mika kai ga hukuma ko dayake cikin mamuyachin hali shi kansa ya zabi yayi biyayya da Allah fiye da mutuum (1Bitrus 2:13-15, Ayyukan manzana 5:29).

Domin gwada holaswa na mika kai ki zabi kullum da kuma kowane lokachi kiyi rayuwa cikin mika kai ga Allah da nufinsa.


Mika kai ga mijina na ko ga shugabana ko kuma ga hukuma zai zama mani da sauki idan na fara zaben yin rayuwa cikin mika kai ga ubana wanda ke cikin sama.

8. **HIDIMA**

Yin rayuwa hidima yana da banbanchi da yi zabi ki bauta ma wasu.

Hidima na yabon kai yana fitiwa ne daga tunanin mutum wanda tana nemah a sansanche ta alama gode mata tana kuma zaba wanda zartayi mata tana da kuma laokachi hidiman, wanda yakan shadi yanayin ta na dan lokachi. Hidiman bi na gaskiya yana tsirowa ne daga dan gantaka na da ubana wanda ke kunshe cikin sirri wanda yake hidima ba tare loakari da matsayi ba, kuma yanayin rayuwa ne, ba abinda aka kelleche ba. Saanda mun zaba muyi Bauta har yanzu mune muke ragama, amma saanda mun zaba mu zama bayi mun mika wannan dama kenan da muke dashi. (Matta 20:26, 23:11, markus 10:43).

Yesu shine ya sarrafa rayuwa hidima (markus 10:45), ba tawurin mutuwarsa abisa giciye ba ko tawurin wanke kafafan almajiransa amma har ma da sauraron zukatan wadanda ke kowaye dashi yana kuma biya musu bukatansu (luka 7:1-17, markus 5:1-42). Ya sami isasshen lokachi da almajiransa, ya ci tare dasu, ya zauna tare da su ya koya musu, ya amsa tambayoyisu, ya kuma masu iko, duk da shike basu zama cikakku ba. Ya bauta ma mafi kankanta wato yara da mata , da masu dauke da aljanu, da wadanda aka fitadda su cikin alluma, ba tare da kuyawa da ko shi wanene ba.sukamakon rayuwan hidima ta gaskiya sune kasanci, musun jkai, da kuma yarda Allah.




## SASHI NA 3: HORAS DA JIKI

9. **AZUMI**
Horaswa ta azumi shine ka guji cin abinci, (ko na ruwa, ko na ci, amma banda ruwa) domin wasu dalilai na ruhaniya. Azumi sama sama shine a guji wasu abinchi (Daniel 10:3)
Dokan tahudawa ta bukachi jama'a suyi azumi sau daya a shekara wato ranna gafaran zunubai. A sabon alkawari babu dokan ayi azumi amma Yesu yace bayaswa da azumi da addu'a ayyukan sujada ne (matta 6:1-18). Kudurin yin azumi, kudiri ne na kadaichi, ko dayake wasu ikklisiyu suna karfaf lokachi yin azumi gaba daya. Dalilin yin azumi shine ya taimake mu ga Allah, ya kuma bayyan abubuwa kamar fahariya da zari ko furshi da yakan mallake mu ya bada bayani xikin jagoranchi da iko wajen yi ma mutune da kasashe addu'a. maimakon ci manufan shine a sami lokachi cikin addu''a da swada idan jikinka na bukatan a kosadda shi yi anfani da wannan doimn tunatarwa yin addu'a ki kuma bada dama ruhanki ya mallaki jikinki. Raayi na daga ganewa na shine muhinmacin lura da halin zuciyarki yayin da kina azumi yafi kyau ki zama da sauki wajen maamala da juma'a maimakon nuna kiyayya garesu. (ishaya 58:4,6-8). A cikin takardansa mai suna, "Bukin Horaswa" mai rubutun *Richard Foster* ya bada shawara cewa wadanda suke koyon wannan horaswan a lokachi na farko sukan fara sau daya a mako na makonni wato bayan abinchin rana sai bayan awoyi 24 kuma kafin wani abinchin ranan, da kuma yin amfani da ruwa lemo da kuma ganyaye domin karya azumi a rana ta biyu. Sa anan sai ki gwada ainihin azumin na tsawon awoyi 24 kina shan ruwa mai yawa. Domin yin azumi mai tsawo kina bukatan ki karanta shawarwari na wasu ko kuma kiyi Magana da wadanda suna azumi a koyaushe. Jaruman azumi a litafi sune MUSA, DAUDA, ILIYA, DANIEL, HANNATU, BULUS Da YESU kansa. Binciken abinda suka yi da dallilin da yasa sun yi azumi, sakamakon zai zama abin sha'awa domin shiryawa sosai.
10. **SAUKIN KAI**
Saukin kai tana nufin rayuwa da ALLAH kamar kome a rayuwwamu, ba mallakanmu ba, ba mutane ba, ba ayyuka ba, amma ALLAH da kansa. Idan muna rayuwa cikin saukin kai, maganan mu zai zama gaskiya da yarda. Ba mu damu da sauran matsayi ko kuma mu faranta ma mutane rai ba. Abinda muke dashi shine zamu ba wasu, domin mun bada gaskiya cewa duk abinda muke dashi na ALLAH ne, wanda ya bamu ranche kamar wakilansa.

Akan ci moriyan mallaka a hanya mai kyaw ba daukar hankali ba (mai wa'azi 6:18-19) mu kan dauki kudiri ne bisa ga abinda muke tunani Allah na bukatan muyi, shiyasa kayayyaki basu mallakan mu, ko raayin mu ko tsoro ko son zuchiya, ko damuwa ko kwadayi da kyashi. Ba lalle ne mu bada dukan mallakan mu ga matalauta ba, an rigaya an badashi ga Allah domin aci moriyarsa a hanyanda Allah ya nuna. Yayan mu ba masu gadon rashin nasaran mu bane, amma kyauta ne daga wurin Allah domin mu rene su ga mulkinsa. Horaswa na saukin kai shine "ka fara bidan mulkin sama da adalchinsa" (matta 6:25-33).

## 11.FARIN CIKI

Kodayake ba a cika sauya farin ciki acikin jerin horaswan ruhaniya ba, akwai nasossi da dama da suka ambache ta, wanda yasa na sanni tabbachi na muhinmachinsa a lafiyan ruhaniyan mu. Yana da kyau mu "bada godiya a kullum kuma cikin dukan yanayi" (1 Tasalonikawa 5:18) sa'anan, "mu shiga kofofinsa da godiya, mu shigo gidansa da yabo" (zabura 100:4). Wani hanya ne yafi da ki gode ma Allah domin abubuwa guda biyar da Allah yayi maki kafin yau. Zai iya zama wani kyauta na iyali, wakan tsuntsu, ko ansa addu'a, ko lafiya, ko yanci ko kariya ko wasu kalaman karfafawa daga aboki, ko wani ganewa daga cikin kalmarsa, ko kuma wani abin kirki daga bako.
A kullum ki koyi halin duban Allah cikin aiki da yanayinsa ko abubuwan da zaki gode masa, ki fara mika godiyanki zuwa ga wadanda ke kewaye dake, dangi ko abokan aiki ko makwabta ko abokan chiniki, jami'an tsaro, da wadanda suke a hidima. Bari su sani cewa da kalaman karfafawa ko dan karamin kyauta yana da muhuminchi a gareki, kuma rayuwansu yana kawo banbanchi arayuwan wasu. Ki kare yaranki, yayinda zaki kwanta ki yi barchi da dare da zuciya na nuna godiya, ki gode masa har ma da mawuyachin lokachi da kika samu, ki koya ki zama da "koshiya da raunana, da zagi, da mawuyachin lokachi, da tsanani da masihu". "gama sa'anda nike raunan, lokachin ne nike da karfi" (1kor.12:10), marubuciya Ann Voskamp cikin takardata mai take "kyautuka dubu daya" ta kalubanci kanta ta buga kyautuka dubu daya daga wurin Allah wanda zatayi farin ciki, hanya mafi ban mamaki da zata bunkasa horaswa rike "halin nuna godiya" (Voskamp 2010).




## 12. KARAMCHI

"Ubangiji yana kaunar mai bayarwa da yardan rai" (2.korintiyawa 9:7). Wani ya taba cewa bamu zama fiye da shi ba saanda mun bayas. Wannan ya zama bangaren jikinmu, domin shi ubanmu ne sai "Allah yayi kaunar duniya har ya bayar" (yohana 3:16). Idan muna masanan bayarwa, sai nan da nan tunanin mu yazo kan kudi, amma ruhun karanchi ya motsa mu mu bayar fiye da bude jakan mu. Da gaske ne Allah yana so mu ba godiyayyu. Kabawar sharia 15:11 ya gargade mu "mu bude hannayen mu ga yan uwamu, da mabukata da matalauta a kasarku" cikin Ezekiel 16:49 mun karanta cewa, bachin ran Allah akan Sodom shine sun ki su kula da matalauta.
Amma kuma Allah yana so mu zama da karanchi da lokochin mu da kuma baiwan mu, da kalaman karfafawan mu, da mallakanmu da kuma hikiman mu. 1timotawus 6:18, ya takaito mana shi da kyau "su kasance masu hannu sake".

### HADDACEWA

- Zabura 119:105: maganarka fitilace wadda zata bida ni, haske ne kuma akan hanyata.
- Irmiya 29:13: zaku nemeni ku same ni, idan kun neme ni da zuciyz daya.

### MABUDIN GASKIYA:

Babu wani bukata ki zama a 'manne' cikin dangantakanki da Allah. A kullayaumi yana jiranki da hakuri domin ki nemeshi da dukan zuciyanki a sabobin hanyoyi, a hanyan da kina binciken maganarsa, yadda kina samun lokachi dashi cikin addu'a, da nuna masa godiya da yadda kike tafiyadda lokachin shirinki, ko kuma duk abinda Ruhunsa ya motsa ki. Bari kowane rana ya zama labara tare dashi yana jagoranta.

## MARTANIN KI:

1. Ki tuna yin binciken litafi maitsarki kan binbini, abinda muke binbini akai da kuma amsan da muke sa rai zamu karba. Sa'anan ki gwada wannan binbini na ruhaniya da kanki sai ki bayyana abinda kika koya. Wani asiri ne kika koya da ya taimake ki yin binbini cikin nasara? Wani tsaiko ne kika samu kuma yaya ne kika yi nasara da su?
2. Ki kwatanta lokachin addu'anki. Yaushe kuma ne kike addu'a? kina da abin koyi cikin addu'anki? Kikan rubuta abinda yazo a lokachin addu'a ne ko bayan addu'a? me yake baki wuya akan samun lokachi cikin addu'a? kina samun shi da wuya kiyi addu'a da karfi a gaban jama'a?
3. Ki duba abinda yake iya yi domin ki saukaka rayuwanki kamar ki rage cin bashi, ki kawas da yawan surutu daga gidanki, ki sayar ko ki bada kyautan kayan da baki amfani dasu kuma.
4. Wadanne hanyoyin bincike ne kika samu masu taimakonki?
5. Ki kan dubi lokachin kadaichi ko kuma tunanin zaman kadaichi yakan sa ki tsorata ko ki damu? Wadanne matakai zaki dauka domin ya taimake ki kici moriyan kadaichi?
6. Wani lokachi ne yakan zama maki da wuya ki mika kanki ga wasu? Kin san ko menene? Yaya zaman krista ya maidoshi da sauki ko da wuya a gareki ki mika kai?
7. Ina ne kike bauta a yanzu? Ki tambayi kanki ko kina zabin kiyi bauta ko zabi ki zama baiwa. Banbanchin shine abinda yake jagoranche ki.

## DON KARIN KARATUN NAZARI:

Bikin Ladabi na Richard Foster (Foster, 1988)

Gidan Almasihu na Zuciya na Robert Boyd Munger (Munger, 1992)

Ceto, mai ban sha'awa da cikawa ta Joy Dawson (Dawson, 1997)

Addu'o'in da suke Amfanuwa da yawa daga Germaine Copeland (Copeland, 2005)

Asirin Addu'a mai ƙarfi na Hammond da Cameneti (Hammond & Cameneti, 2000)

Kyau Dubu Daya Daga Ann Voskamp (Voskamp, 2010)

Shafukan Intanet na Nazarin Littafi Mai Tsarki Kyauta:

www.biblegateway.com

www.blueletterbible.com

www.netbible.org

www.e-sword.net

www.lovegodgreatly.com

**DARASI NA 6: SHUGABANCHI TA BAWA**

Labarin shugabancina ya fara ne sa’anda nike kaunar diyar pasto na fara hidima a matsayi daban daban a ikklisiya, ina taimakawa a ajin yara da fannin choir da kun giyan matasa, koyaswa a makarantan lahadi, da kayan kide kide, har ma da sharan ikkilisiya bayan sujada. Hidima a matsayi, daban daban yana da kyau, naji dadin koya, ina kuma so in koyas. Karuwar nawayya akaina a lokachin da nike koceji ya zam mani na hallita. Bani da bukatan in zama ‘shugaba’ ko mai ‘ganin ruya’ amma na gansu da goyon bayan shugabanchi da kuma bauta. Shekaru goman da nayi kaunar uwa ga yarana maza biyu sun koya mani abu da yawa game da shugabanchi da kuma bauta, amma kuma a lokachi da nayi shekaru ashirin ne cikin hadoddiyar duniya, yayinda na tashi daga matsayin shugaban kungiya zuwa mai duban aiki, daga nan na zama manaja a lokachin ne yanayin shugabanchi ya bayyana. Na sani ba nine na chanchanta in zama manaja a kanfanin da maza ne sun fi yawa ba, amma na koya cewa mutane da suke a sashe na sun fi yi da kyau idan an basu inda ake bukata sukai sai nayi duk abinda zan iya yi domin in kawas da kowane tsaiko da yake hana su cimma burinsa. Na saba wannan kalman cewa “shugaban bawa” kuma da na ba ma kaina wannan taken bisa ga abinda na sani, amma chan cikin zuciyata ina maida kaina shugaba na aji biyu ba kwararren ba, wanda ba a haife ta da kashin shugabanchi daga halite, amma na koya inyi tasiri a wannan gefen. Sa’anan na karanta takardan Robert Greenlead mai take “Shugabancin Bawa” sai nayi karo da wannan: shugaban bawa, shi bawa ne da farko. Yana farawa ne da ji na hallita cewa mutum yana so yayi bauta, bauta da farko. Sa’anan lamiri ya kawo mutun ga ji Yayi shugabanchi. Wannan mutumin yana da banbanchi daga wanda

yake shugaba ne da fari. Banbancin yakan bayyana kansa tawurin kula da bawan yayi da farko, domin ya tabbatar cewa babban bukatan mutane ya mu biya. Gwagi mafi kyau shine, wadanda suke bauta suna girma kamar mutane? Suna samun lafiya ko hikima ko a sake ko yancin kai, ko kuma mai yiwuwa su zama bayi yayinda ake bauta musu? (GREENLEAF, 1977 P.27) Yana cewa ne, ni kamar shugaban bayi ban zama na biye da mafi kyau ba. Wannan tunani ya zama mani hasken wuta ne alokachin. Sai na fara gane shugababci a wani gefe ne daban.

Mata da yawa kamar ni na koyi aikin bauta sosai, har naji dadin biyan bukatan wasu. Ko Allah yana kiranki yanzu domin kiyi wannan zabi na shugabanchi? Ina so in karfafaki domin ki dauki wannan mataki na bangaskiya. Ki bada kai domin ki jagoranchi su wajen bin ciken litafi mai tsarki, ko ki shirya wani shiri ko kuma ki shirya wani kungiya domin cimma wani buri. Idan Allah yana kiranki, zai baki kayan aiki domin yin shi.

Wasu mutane zasu yi gardama cewa tunanin bawa da na shugaba ba iri daya bane. Yaya mutum zai zama shugaba da bawa a lokachi guda? Ansan Yesu ga wannan tambayan yana nan a Luka 22:26, "sai dai wanda yake babba a cikinku ya zama kamar karami, shugaba kuwa ya zama kamar mai hidima". Ba kawai ya tabbata dashi da kalamominsa bane, "kamar yadda dan mutum ma yazo ba domin a bauta masa ba sai dai domin shi yayi bautar, ya kuma bada ransa fansa saboda mutane dayawa" (mat 20:28) amma ya bar mana abin koyi lokachin rayuwan sa anan duniya.

1. YESU KAMAR SHUGABAN BAYI
   Yesu shugaban bayi ne na gaske a tunaninmu na yau? Shugaban bayi yakan nemi ficewa da kuma sa zuciya domin bunkasa mafi kyau da mafi daukaka cikin mutane. (Spears, 1998, pxii) lallai babu shakka a wannan matakin ne yake. Halayan wasu shugabanin bayin kuma fa (Spears 1998, pp 4-6)? Ga misalai kamar haka:
   1. Sauraro: shugaban bayi sukan saurara da kyau ga raayoyin wadanda suke shugabanta. Yesu ya saurari wadanda suka zo wurinsa, ya amsa tambayoyinsu, harma a lokachin matsuwansa (Yohana 3:1-21, 4:7-42).
   2. Juyayi: yesu yaji juyayi akan dukan wadanda yake shugabanta (Matta 9:36, Luka 7:13).
   3. Warkaswa: shugaban bayi sukan taimaki wadanda suke jagoranta su warke. Allah ya shafe Yesu Kristi banazaret da ruhu mai tsarki

NOTES

da iko. Ya tafi yana warkas da dukan wadanda shaitan ya nawaita su. Ayyukan manzani 10:38.

4. Wayar da kai: shugabanin bayi suna da nasu natsuwan zuciya. Yesu ya sani ko shi wanene ya kuma san inda zashi, baya bukatan wani ya tabbatar da haka din, Yohana 2:24-25).

5. Rinjayaswa: shugabanin bayi suna lallashi ne maimakon tilastawa mutane su bi ra'ayinsu. Yesu yasan cewa yahuda zai bashes hi, amma ya bar yahuda ya zama a cikin almarajiransa har ma da nawayyan ajiyan kudi (Matta 26:25, Yohana 13:29, 17:12).

6. Aiwatar da dabara: shugabanin bayi sukan daidaita ayyukan yau da kullum da dabaru fiye da yadda ake gani. Yesu yana yin wa'azi akai akai game da mulkin sama "sai ya zazzaga duk kasar galili yana koyaswa a majamiunsu, yana shelar bisharan mulkin Allah, yana kuma warkar da kowace cuta da rashin lafiya na mutane" (Matta 4:23).

7. Hange: shugabanin bayi sukan yi anfani da darasi da ya wucw abisa darasin yanzu su saurari sakamakon kudurori. Yesu ya gargadi almajiransa game da mawuyacin lokuta masu zuwa domin kansa da kuma su, (Luka 9:44-45, Matta 24:1-31).

8. Wakilchi: shugabanin bayi wakilai masu hikima ne tawurin dukiyarsu, sun dukufa wajen bautan wasu. Yesu tawurin hikimarsa ya saka wa lokachinsa. Cikin shekaru uku ya kawo sauyi ga duniya ya ba da shi ga talakawa amma ya yarda masu arziki su bashi.(Yohana 13:29, Matta 26:7-12, Luka 8:3).

9. Mika kai ga girman mutane: shugabanin bayi sukan karfafa girman ruhaniya da girman aiki ko sana'a na wadanda yake shugabanta. Yesu cikin hakuri ya sanya lokachinsa wajen koyaswa, gyartawa da kuma horas da almajiransa goma sha biyu, yana zuba saninsa a cikin su. (Matta 10:1, 11:1, 16:24, 20:17).

10. Gina allumma: shugabanin bayi suna aiki domin hada kan mabiyansu su zama kungiya daya. Yesu ya

koya ma almajiransa suyi kauna juna su kuma bauta ma juna. Bayan mutuwansa da tashinsa daga matattu sun hadu gaba daya, sun hadu da manufan kai bishara ga dukan duniya (Yohana 13:14-16, Matta 28:19-20, Ayyukan manzani 2:44-47).

Wani misali ne na shugabancinsa na bayi ya zo zuciyarki kuma?

**2. YIN SHUGABANCHI TA BAWA A YAU**

1. Sauraro: ki zama da sha’awan mutanan da kike shugabanta da iyalansu da abubuwanda suke so da abinda basu so, abin da yake sa ruhunsu ya ji dadi da abinda yake sa ruhunsu ya damu, ki saurari abinda suke cewa da abinda basu cewa, kiyi musu tambayoyi na wayas da kai domin ki gane ra’ayoyinsu da dabarunsu. Bulus ya sa shi kamar haka “ku girmama wadanda suke aiki a tsakaninku ku rike su da mutunchi kwarai game da kauna saboda aikinsu” (1 tessalonikawa 5:12-13).
2. Juyayi: Alal misali wadanda kike shugabanta suna maki fata mai kyau, ko da yanayinsu ko kalamansu ba karbabiya bace. Ki gane cewa mutanen da anji musu sama suna ji ma mutane da sanin yadda za’a gafarta da kuma yaushe za ayi gafaran tabbatache ne. ki nuna halin juyayi ga wadanda ake ji musu ko kuma suna fuskantar matsaloli a rayuwansu. A wani lokachi wannan yakan kunshi “hidimar kasancewa”, ki kasance a zaune shiru cikin natsuwa a yayinda suke damuwa. Kamar mata, mu kan so muyi wani abu, shirya abinchi, ko kuma kula da yara ko sharan gida, amma abinda an fi bukata sosai shine abokiyan tafiya mai addu’a. sai da hikima da kuma bishewar ruhu mai tsarki ne zaki iya gane ko wane ne martani na juyayi a kowane yanayi.
3. Warkaswa: ki taimaki wadanda kike shugabanta su sami warkaswan ruhaniya, da na hankali da na tunani da kuma na jiki. Mai yiwuwa bamu da dubaru da zamu warkaswa ta jiki ga wahala, amma idan mun saba da “Babban Likita” zamu roka a madadinsu. Ga wadanda suke da damuwa ta zuciya da ta ruhaniya ko kuma anji ma hankalinsu, shugaban bawa zai yi musu kalmomin albarka da karfafawa da kuma bege.
4. Wayar da kai: cikin addu’a ki gane naki kasawan da rashin daidaita da yin zunubi kamar shugaban bawa ki san ke ko wacece ko na wanene, martabanki, da hanganki da kuma kiranki. Idan jaraba yazo domin ya hura ki da fahariya tawurin yabonki dasa wajen wasu, ko kuma a shafe gaskiya domin ya nuna ki da kyau ko ki kewaye kanki da wadanda kawai sun yarda dake, sai ki bada dama ga ruhu mai tsarki ya falkadda lamirin ki ya dawo dake kan gaskiya.

5. Rinjaswa: kokarin rinjayan mai bada kai ya bada lokachinshi da baiwansa domin ya cinma manufansa yana da wuya sosai fiye da rinjayan mai aiki da kin dauko yayi maki irin aikin. Masu bada kai suna bukatan karfafawa a ko yaushe. Suna so su ga muhimincin aikin da suke yi. Na koya cewa wadanda suka samu ji su mika kansu domin aikin mika kai saboda Allah ya kirasu ga wannan aikin suna da jimrewa kuma suna dadewa a cikin fiye da wadanda an sa su aikin. A wata hanya idan wani yana jin kira amma ba daidai yake domin aikin ba, rinjayaswa da karfafawa sun zama muhinmi ne. Tilastawa ba wani ra'ayi bane ga mai bada kai.
6. Aiwatar da dabaru: domin iya aiwatar da wahayi a bayyane wanda AAllah ya baki. Wanda zai dauki aiki da koyo, amma kuma kudurin ba zai zama a banza ba idan wadanda kike shugabanta zasu iya gani sakamakon abinda kin aiwatar. Wannan wahayi zai iza dabarunsu da karfinsu ya kuma taimakesu wajen daukan kudiri.
7. Hange/Hikima: shugabanin bayi wadanda sukan yi antani da dabaru na darasin ya wuce domin yanzu domin dukan kudiri mai kyau ne kuma ya hana su fadiwa cikin ramuka. Kiyi amfani da (Yakubu 1:5), ki roki Allah domin hikima, ki kuma sauya wasu wajen daukan kudiri domin tanada wasu dabaru da kuma ganewa. Idan babu shawarwari, shiri yakan lalace, amma in akwai masu bada shawara zasuyi nasara. (Misalai 15:22).
8. Wakilchi: shugabanin bayi suna anfani da dukiyoyinsu da hikima. Wadatan kudi amana ne daga wadanda suka bayar. Domin kiyaye wannan amana da masu bayarwa, ki bayyana a fili yadda kika yi anfani da wannan dukiya. Ki girmama lokachin da masu bada kai suna bayaswa tawurin zama a shirye da kuma zama a kimtse. Ki kudurta ki gane karfin ko rashin karfin mai bada kai ga walali da hikima.
9. Mika kai domin girman mutane: ki taimaki mutane su gane karfinsu da rashin karfinsu domin su bayyana baiwansu tawurin kwatanci (nunawa), da koyaswa, da horaswa, (gyartawa da kalubalanchi) da kara karfafawa (wakiltawan) su. Horaswa ta kunshi bada sakamako, abinda suka aikata da kyau da yadda zasu ingantu. Ki iza su su gane darajan su, da juyayin su da kuma kiransu. Ki nuna jin ki domin cigaba da koyo da girma, ko da ma zai nuna rashin iyawarki.
10. Gina alumma: shugabanin bayi sukan nuna kauna mara iyaka ga wadanda suke shugabanta hanya mafi karfi da za a gina alumma shine tawurin kirkiro kauna mara iyaka, yayinda kike rayuwa mai sauki, da kwarjini da farin ciki da juna. Zaki iya karfafa su da baki domin su rika taimakon

juna, sa'anan ke kuma ki nuna, kuma nuna musu yadda wannan yake tawurin bayyana kauna garesu da kanki yana da inganci da kuma karfi sosai, koda kuma ki manta ku rika jin dadi tare. Ki yarda su san cewa kina jin dadin zama dasu.

Kada ki raunan idan baki gan sakamakon shugabancin bawa ba nan da nan. A cikin takardan Stephen Covey ya rubuta Mai Take "Hange a Shugabanchi" ya kwatanta shugabanchi bawa da wani itace a kasar china.

> In kin shuka shi bazaki san wani abu ba sai wani dan karamin alaman tsiro da zai kunno kai har tsawon shekaru hudu. A cikin shekaru hudu din nan sauyoyin wannan itacen sun sami kafuwa sosai har can cikin kosa mai zurfi, amma duk da haka bazaki gan komi a waje ba. Kina aiki tukuru a koyaushe. A shekara na biyar wannan itacen sai yayi girma kafa 80. (spears, 1998pxviii).

**HADDACEWA:**

- Markus 10:45- domin dan mutun yazo ba domin a bauta masa ba, sai dai domin shi yayi bautar, ya kuma bada ransa fansa saboda mutane da yawa.

- Matta 25:40- sai sarkin zai amsa musu yace, hakika ina gaya muku, tunda yake ku yi wa daya daga cikin wadannan yanuwana mafi kankanta, ai ni kuka yi wa.

**MARTANIN KI:**

1. Kin maida kanki zama shugaban bayi? In haka ne don me in kuma ba haka ba don me? Me yakan zo

NOTES

maki da sauri cikin wadannan, bauta ko shugabanchi?

2. Cikin kaidodi goma na shugabancin bayi da muka zayyana, wannene ya zama maki da kalubalanci da kuma wanda ya zama maki da sauki?
3. Ko kina tunani shugabanchin bayi bai yi aiki da kyau a wasu al'adu ba?.

**DON KARIN KARATUN NAZARI:**

Jagorancin Bawa na Robert Greenleaf (Greenleaf, 1977)
Fahimtar Jagoranci na Larry Spears (Spears, 1998)
Jagoranci Daga Zuciya na Jack Kahl (Kahl & Donelan, 2004)

**DARASI NA 7: DARAJA, ABIN MAIDA HANKALI , DAIDAITAWA.**

Misalign Yesu akan talent cikin Matta 25:14-30 ya kan zama mani da tashin hankali a ko yaushe. Na gane da farko irin talent da Allah ya bani, amma tambayan da yake ta damuna a duk sa'anda na karanta wanna misalign shine, "Allah menen kake bukata daga gareni?" Bana so in zama kamar bawan nan da ya boye talent nasa. Ina gani kamar a kowane lokachi na rayuwa akwai ababa da dama da na aiwatar, amma yanzu suna zama a zube, ko kyautai da nike tunani Allah ya sanya a cikina wanda ban rigaya ba bunkasa su ba.

Ya cigaba da zama haka a irin wannan lokachi a rayuwa, cewa naji Allah yana rokona in koma inje in dauki wadannan abubuwa da suka fadi domin ya maida su cikakku. Menene wannan baiwan da Allah ya sanya cikinki wanda yake bukatan kiyi anfani dashi domin tadada mulkinsa? Mai yiwuwa wani lokachi kinaji a mike da abubuwa masu yawa domin dai ki gani kin iya aiwatar da abubuwan da ya kamata ki aiwatar a kowane rana. Inaso in karfafaki da ki bude idon ki da ruhunki ki gan abinda Allah zai yi tawurinki. Wannan darasi ne game da lokachi da maida hankali da daidatawa da kuma gano abinda yake da daraja gaske daga wurin Allah.

1. **KI SAN MUHIMMANCHIN KI:**
   Menene kika fi martabawa a rayuwa? Menene yake baki farin ciki ya kuma sa ki jin dadi? Ki rubuta abubuwa uku ko hudu amma kada ki rikitadda shi ko ya zama wani iri. Kada ki dami kanki da wani tunani daban ko ki tambayi wasu abinda suke tunani ya zama da muhimmanchi a gareki Ki fadi ma kanki gaskiya kawai. Wanna domin idanun ki ne kawai, sansancewan abin da kin sani cewa gaskiya ne a zuciyarki. Idan baki san inda zaki fara ba, ki roki Allah domin hikima da ganaswa kada ki damu idan baki samu nasara a

farko ba ko kuma kin sami wani tsaiko da ya hanaki gamawa a zama nafarko, amma ki adana abubuwan nan da kika rubuta a wurin da zaki rika bin cika shi, ki kuma bayyana shi, ya zama maki da sauki, da bayyanannen abinda ya zama maki da muhimmanchi.

Tawurin misali, ga yadda na amsa wannan tambaya:

- Dangantaka na da Allah da iyali
- Tallafa wa wasu: kauna, da koyaswa da karfafawa da kuma mika alheri.
- Aikin da za'a cinma buri amma masu kalubale.
- Yanci domin sanin gaskiya da martaba da kamewa.

Me zai sa ki rubuta dabaranki? Idan kin iya kin nuna su zasu taimake ki wajen daukan shawara hakannan kuma da yanayin ki a kullum.

## 2. KI KAFA KI KUMA YI RAYUWA AKAN ABINDA KIN FI MAIDA HANKALI.

Ga yawancin masu bi da sun yi girma, abubuwa guda biyar da za a fi mayar da hankali garesu sune: Allah, abokin zama, yara, aiki, da ikklisiya. Wasu abubuwan maida hankali kuma sune kamar haka, yan'uwa, abokai, kanki, abinda kikafi so, ilimi da dai sauransu, har sai mun kai karshe idan muna kirga, amma kuma zaki iya samun wata yar matsala kamar karamin yaro ko wani yaro da yake da wata lallura ko tsafaffi wadanda zasu daga wannan mutumin har rayuwansa.

Na farko: me ake nufi da cewa Allah shine na Farko a rayuwa na? Dangantaka na dashi shine ya zama na farko a rayuwana. Amma wannan ba yana nufin in guji nawaya na na iyali, in bata lokachi na duka cikin dakina ina addu'a ba, amma a kullum ina neman nufinsa ina kuma biyaya da maganarsa domin in iya taimakon mijina da iyayena da kuma yarana.

Na biyu: Na biye sai abokin zama na. mika kaina gareshi na dukan rayuwa na ne sa'anan yarana kuma ranche ne gareni daga wurin Allah na tsawon shekaru ashirin ko kuma kosa da haka. Idan yarana sun zama na biyu ko na farko, dangatakana dasu zai zama da nauyi da ba zasu iya dauka ba.

Na uku: burina kamar uwa shine in tada manya na ruhaniya da na kudi dana hankali masu dogara da kai da masu daukan nawayya wadanda suna kaunar su bauta ma Allah. "sai dai ku goye su da tarbiyya, da kauna gargadi ta hanyar ubangiji"(Afisawa 6:4). Su ba kayan nasara da zasu sa ni inyi doro bane, ko kuma shaida ne na iya tarbiyya ba. Amma mutane ne wadanda anyi

cikin kamanin AAllah, wadanda suma suna da nasu zabi, suna kuma da nasu buri, sa'anan kuma cikin addu'a suna kafa nasu dangantaka tare da ubansu na samaniya, wanda shi kadai ne kawai zasu amsa masa.

Na Hudu da na Biyar: Ni dai a gareni, aiki da Ikklisiya sun zama mani daidaitattun buri. A wasu lokatai ikklisiya takan zama mani abinda zan fi maida hankali, wani lokachi kuma aiki yakan zauna mani haka din, ya danganchi nawayyana ne a wannan lokachi. A sashen ikklisiya, na bada gaskiya cewa ba zamu fasa taruwan mu ba, da shike Allah ya kiramu muyi rayuwa cikin alumma da muke da irin bangaskiya daya. (Ibraniyawa 10:25). Kaunarmu ga juna cikin jikin Kristi shaidan almajirancin mu ne, yadda yake shine aiki mafi kyau (Yohana 13:35, 1Bitrus 2:18, kolosiyawa 3:23). Akwai wasu lokatai a rayuwan mu wanda mukan fuskanchi wani yanayi ko kuma ruhu na Allah yakan jagoranche mu domin muyi wasu gyare gyare, amma wadannan sune mataki masu anfani ga kowa kamar masomin kafa burin mu. Tambaya mafi wuya shine, ko hanyan da muke anfani da lokachin mu yana nuna wannan buri, kowane rana kyauta ne daga Allah wanda zamu bada lissafin sa. Ba za'a sake bamu wani wannan ranan ba. Yadda muke anfani da lokachin mu, abin tunani ne a gareshi (zabura 90:12).

An rubuta takardun sana'a da dama wanda ake bada shawaran anfani da dabarun ajiye lokachi, akwai kuma sana'a da sun shahara wajen rubutu a takarda ko tawurin na'uran contraki ko na'uran konfita domin su taimake ki ajiye lokachi da kyau, amma a karshe na gane cewa abubuwan da sun zama muhinmai sune: wasu ka'idodi na asali, ko kalanda ko takardan daukan rahoto da kuma zuciya da take hade da ruhu mai tsarki.

1. Kiyi amfani da kalanda ko wani shiryayyen takarda domin ki cire sa'awoyi da makon'ni da basu da ayyuka da yawa. Cikin shirinki ki sanya cin abinci da barchi da aiki da kuma motsa jiki da lokachin sujada da ayyukan ikklisiya da kuma ayyukan gida na yau da kullum har da zuwa kasuwa, da dai sauran wasu ayyuka na mako da na wata. Ki kebe ranar lahadi kamar ranar hutu da walawa da iyali in ya yiwu. Wurin da kika bari zai zama lokachi ne domin ayyukan da zasu iya tasowa, idan wani yace miki kiyi mashi wani abu ko kiyi tare dashi ko ki kudurta ki cusa kai sosai, ba damuwa ki gane cewa hakan ya fitone daga lokachin da kika bari ba komi a mako.
2. Abu na biye shine ki dauki lokachi kina shiryawa kina kuma harhada yadda zaki yi aikin gida domin takaita lokachin da zaki bata a kansu. Akwai wata kaida da tace, aiki zai dauki yawan lokachi da kin bashi.

Kiyi addu'a domin hikima. Idan awoyin sun kasa miki a mako, menene zaki bayar ga wani a iyali domin a taimaka maki? Wane ayyuka ne zaki iya hadawa ko ki banbatasu ko kuma ki cire gaba daya cikin ayyukanki? Dukan mu kowa yana da lokachi mafi kyau wanda mukan yi aikin mu da kuzari, ga wasu wannan lokachi yakan zama da safe ko da rana ko ma cikin tsakiyan dare. Ki sansanche ko wadanne lokachi ne kin fi yin aikin da kuzari sai ki zaba a natse abinda zaki sanya a irin wannan lokachi. Ki kuma sansanche masu bata lokachi wadanda suna cinye ranan ki kamar rashin hada abubuwa da katse maki hanzari, da rikichi da kuma jinkiri da rashin aiki.

3. Manufan wannan shine a kara kirkiro lokachin da babu ayyuka sosai domin abubuwan da sun zama dole amma ba a gaggauche ba wanda zamu iya dagawa a kowane lokachi, abubuwa kamar karatun litafin da zai kosar da ruhun ki, ko kuma sharan dakinki, ko kuma shan shayi da abokiya, ki lura yadda zaki yi anfani da lokachinki da babu ayyuka sosai, kina karbar sabobin nawayoyyi da addu'a da kuma ganewa abinda yasa kike karban kiyi haka din.
   Yanzu kina gude ne da manufa (1korintiyawa 9:24-27).

## 3 AYYUKAN DAIDAITAWA

Daya daga cikin alamura masu wuya da mata suke fuskanta shine yin daidaituwan rayuwa, nawayya a wurin aiki da gida da kuma ikklisiya, tana kokari tayi dukan su da kyau da kuma gaskiya, tana kokari domin tasa kowa yayi farinciki. A gareni rayuwa ta zama mani da sauki da kuma daidai tuwa sa'anda na gane cewa nawayyana ne da kuma aikina ne in sa kowa yayi farinciki. Wannan zai zo ne daga dangantakarsu da Allah. Zan iya tanada abinchi mai lafiya, da gida mai kauna da ta'aziya da karfafawa da hikima da kuma bege, amma b azan iya sa suyi farinciki ba. A gareni, daidaitawa tana zuwa sa'anda na gane cewa nayi rayuwa a gaban masu sauraren mutum guda, ba na  faranta ma kaina ko wasu, amma Allah da kansa. A wani lokachi wannan yana nufin cewa ki zabi ki kasance a wurin wasan motsa jikin yaron ki maimakon halartan taron addu'a ko kuma gina dangantaka, a wani lokachi yana nufin shirya ma iyali abinchi da dare kafin da safe da zan yi tafiya don aiki ko kuma ki hada binciken litafi mai tsarki a gidanki maimakon aiki a makare. Kowane rana ya zama da daidaitawa aiki, karfin hali cike da addu'a. da gaske, akwai faduwa da kalubale a hanya amma a karshe zan iya cewa, tawurin amincin say a jagoranche ni a sawun tafiya ta. Ba da na sani.

Akwai lokachin da na taba yin kuskure? Lalle kam. Na koyi wannan sa'anda ina bakin ciki, sa'anda ina fama da yarana ko ma'aikata na, sa'anda zuciya na yana kan zagayawa tun ina kwance a bias gado ina kokarin barchi, yakan zama haka domin abin da nasa a gaba bashi a hanya. Lokachine da zaki sami wuri a kadaiche kiyi binbini da kuma tuba da sake gyartawa. Allah kasan cewa awa ashirin da hudu (24) ne kawai a rana. Ba zan iya yin dukan wadannan abubuwa ba. Menene abu mafi muhimmanchi da ya kamata inyi nan gaba? Rayuwana ta kauche daga inda zata, domin ina yawan bada dama ga abubuwan gaggawa ko kuma mara muhinmanchi su faru su fi karfin abinda nasa a gaba da kuma daraja.

Idan kina gwagwarmaya samun daidaitawa a rayuwanki kina damuwa akan jerin ayyukan da kin shirya fiye da awoyi a rana, zan so in karfafa ki ki sani lokachi cikin addu'a ki nemi ubangiji domin chanjin da ya kamata a samu a rayuwanki. Yesu yace, "Bauta fa sassauka ce kayana kuma marar nauyi ne" (Matta 11:30). Idan karkiyan kin a nawayya yafi karfin abinda zaki iya dauka, ba shakka kin dauki fiye da abinda ya kiraki kiyi. Ki tuntubi iyalinki da wadanda kin yarda dasu domin shawara. Zasu iya baki wani tunani daban ko kina cikin yaki na ruhaniya kina yaki da abokin gaban ranki? Kina neman matsayi fiye da shirin Allah? Kin dauki nauyin da bai kiraki kiyi ba? Ke kadai ne zaki amsa wannan tambaya da Allah yana jiranki kiyi tambaya.

"Aikin da Allah yayi tawurin mu ne ya kamata, ba abinda munyi masa ba" (Chambers, 1992,P.august 30.).

**HADDACEWA**

- Zabura 90:12- ka koya mana mu sani ranmu na dan lokachi ne, domin mu zama masu hikima.
- Misalai 24:3-4 An gina gidaje akan harsashin hikima da fahimta wurin illimi akan kawato dakuna da kyawawan kayayaki masu tamani.

**MABUDIN GASKIYA**

Sanin darajan mu da kafa burinmu bias ga maganar Allah yana da mahimanchi idan muna so muyi rayuwan daidaitawa ga tunanin Allah.

## DARASI NA 7: DARAJA, ABIN MAIDA HANKALI , DAIDAITAWA.

**MARTANIN KI:**

1. Ki rubuta yanayin darajanki na yanzu sai ki ajiye shi a wurinda zaki iya ganinshi domin kiyi koyi dashi a koyaushe sa'annan a loto loto a rika waiwayansa.
2. Akwai wasu baye baye ne ko iyawa da kina tunani Allah zai bukace ki kiyi a wannan lokachi, amma baki iya aiwatar dasu ba domin kin rasa lokachi ko kudade da zaki aiwatar dasu? Idan haka ne, kamar su menene? Wani mataki ne zaki dauka (faraway da addu'a) domin fara bude kofofin?
3. Kin sansanche wadannan abubuwa da kinyi da na sani da yinsu. Ki cika wadannan mika kai wadanda sun zama hidima ne na lokachi guda. Ki fara cikin addu'a kiyi aiki kan shirinki a saukake da mika kai ga abinda kika zayyana. Zaki iya samun wani wanda zai cika burinki ko kuma ki iya samun Magana da wani wanda kin bada kanki akanshi yayi aiki dasu, ko kuma Allah ya baki wata hanya, ki fara shirin sansancewa da addu'a yau.

**DOMIN KARIN KARATU:**


Margin ta Richard Swenson (Swenson & Swenson, 2002)

The Balanced Life by Alan Loy McGinnis (McGinnis, 1997)

Dabi'un Bakwai na Mutane Masu Inganci Na Steven Covey (Covey, 1989)

Gudanar da Lokaci daga Ciki daga Julie Morgenstern (Morgen, 2000)

Samun Zuciyar Maryamu a Duniyar Martha ta Joanna Weaver (Weaver, 2000)


**DARASI NA 8: SADARWA, MUTANE, YANAYIN DANGANTAKA.**

Babu abinda yafi yin kudiri ga shugabanchi mai nasara fiye da sadarwa mai inganchi, babu kuma abinda yafi kuduetawa ga sadarwa mai inganchi fiye da gane ma su sauraronka. Sadarwa ya wuce yin magan kawai, yare ne na jiki, ko murya, da kuma bayyana manufa, da kuma sanya abindda kike fada shine masu jinki suke ji . zaki yi Magana, amma idan masu jinki basu iya yarenki ba ko kuma basu gane yaren ki ba, to baki yi sadarwa ba.

A wannan darasi zamu bada shawara cewa ba yaren mai jinki ne kadai da muhimmanci ba, amma mutuncinsu. Mutane biyu zasu iya jin sako iri daya daga mutum daya, amma kuma zasu fassara shi daban dajuna bias ga yanayin su. Zamu yi Magana akan abubuwa guda hudu na yanayin mutum ko halin mutum da aka gano fiye da shekaru dubu biyu da suka wuce, har yanzu yana nan a yadda yake. Gane baiwan sadarwa da kuma mutunchi suna da anfani idan zamu tada kungiyan da tana da dangantaka mai ma'ana da jama'an ma.

1. **SADARWA**

   Kamar shugabanai mukanyi tunani akulum cewa sadarwa hanya ne na kaiwa ga wadanda muke shugabanta. Akwai iko cikin furchin harshe da motsawa ga dubban masu sauraron ki, amma kuma akwai ikon dangantaka cikin sauraro mutum da mutum.. sai fa in muna sauraron masu jin mu ne zamu iya sani ko suna fahimtan mu. Wani marubuchi mai suna *Steven  Covey* ya bayyana muhimanchin sauraro a cikin halinsa na biyar a takardan da ya wallafa mai suna "HALAYE BAKWAI NA INGANTATTUN MUTANE




yace Ki fara bidan ki gane, sa’anan zaki gane” (Covey, 1989) ya sake bayyana cewa a yau da kullum, maimakon sauraron wasu mutane, cikin hankali mu shirya martanin mu. Ya kuma bada shawara cewa zamu zama masu sadarwa mafi inganchi idan muka saurara da kyau mu kuma sake duba abinda wasu mutane suke cewa mu kuma tabbata mun fahimche su. Misali zamu ce “ina tsamani kina cewa ko na fahimce sosai’? Sa’anda na fara koyon wannan kaida na sami wata zarafi nan da nan domin in gwada shi a kan wasu yarana wadanda a lokachin suna tasowa ne da yanayi daban da kuma tunani daban daban. Wata rana da yamma a lokachin abinchi dare da muke tattaunawa sai na umurni kowannensu suyi amfani da dabarun Covey. Wannan ya kaimu ga maganganu daban daban, shugabanai da suke marabtan sabobin ra’ayoyi da kuma kalubale a kulayaumi zasu saurari sakamako, yabo da kuma sukan ra’ayi. Yadda ke kamar shugaba zaki saurara ki kuma mayar da martini ga kowane irin Magana zai bayyana irin yanayin shugabanchin ki. Zaki kada kai kiyi murmushi bazaki ce komai ba (ba kuma zaki koya kome ba) ko kuma zaki saurara da kyau ki kuma nemi ki fahimchi tunanin da yake biye da abinda an fadi. Idan kuma yabo ne, tawurin saurara zaki iya gane da kyau abubuwan da suke na taimako, idan kuma Magana mara anfani ne, zaki iya gane cewa suna da takamamman dalili. Yana da muhimanci mu san da cewa mutumin da yake gaya maki sakamakon mara dadi yana baki wata baiwace, zata gaya maki zuciyanta ta kuma baki zarafi ki tabbatar, ko kuma ta bayyana ma abokanta guda ashirin da suke kusa da ita. Ki karbi baiwan kowane irin sakamako da farinciki da fahimta. Akan kira shugabanai domin su amsa ma wadanda suke shugabanta a lokachi damuwa da masifu, amma sai ki iske kalilun ne kawai ko kuma duka ma basuda horaswan abinda zasu ce ko zasu yi. Domin gudun kada su ce wani abu ko suyi wani abu da ba daidai ba sai su

guji alamarin gaba daya. Wani kungiya mai suna Stephen Ministry ya tanada hanyoyin horaswa masu kyau a wannan sashen ya kuma kawo shawara mai sauki na "Hidiman Kasan Cewa" Kasancewa kana sauraro ko kuma kina zama a natse da wadanda suke da damuwa yana da matukan kyau kuma baiwa ne.

Sauraro abin kudurtawa ne, amma kuma a lokachi guda, bana so in rege muhimanchi iya Magana a bayyane abinda Allah ya sauya a zuciyanki ga wasu yan bayanai:

a. Idan kina neman na gaske game da yanayin koyarsuwanki, ki koya ma ajin yara, zasu sa ki gane yadda kike.
b. Koyo, Koyo, Koyo! Na karanta cewa Billy Graham Yakanyi ma kututturen ice wa'azi. Mahaifina ya koya mani in koya a gaban madubi domin in iya ganin abinda zanyi ko kuma yanayi na da zai dauke hankali.
c. Dauke shi da sauki ! Wannan ba yana nufin ba zaka shirya bane. Yana ma nufin cewa kiyi cikakken shiri, ki kuma gajarta sakonki zuwa misalai uku ko hudu masu ma'ana.
d. Kada ki damu idan kina saurin jin kunya. Mahaifina, pasto ne na kusan shekaru sabain (70) wanda yakanyi wa'azi sau hudu zuwa sau biyar a mako, ya taba gaya mani cewa duk sa'anda yake wa'azi yakan ji tsoro sai sa'anda kina da gaba gadi a naki iyawa ne ba tare da gane cewa kina dogara ga shafewan Ruhu mai tsarki ba kina cikin matsala.
e. Ki roki Ubangiji ya taimakeki ki zama hanya da kaunarsa da kuma gaskiya zasu bi ki kuma zama Santali mai haske domin haskakawa. Jinki ko tunanin ki a bayan sakon ki ko kuma rashin martani daga masu jinki basu zama alamu masu kyau domin sanin ko sun fahimchi sakon ba.

   Kasancewa gun gun mutane shriru a natse zai iya nuna cewa maganan ta samu shega zukatan su babu dauke hankali ki bada gaskiya ga Allah domin ya tabbatar da manufarsa,Ruhu mai tsarki kuma ya kawo gaskiya ga masuji.

**2. IRIN YANAYIN MUTANI**

Manuhan gane yanayin mutane ba a tantanche mutane zuwa abu mai kyau ko marar kyau bane,amma don mu gane daillin da yasa muke mayar da martani yadda muke yi da kuma daillin da tunani dabam.yayinda muke koyo ganna da wasu,sai mufara ganewa cewa hanyanmu ba ita kadai bace hanya

mai kyau,tunani dabam cikin shiri da kuma biyan bukata zai taimaka wajen samun sakamako mai kyau idan mukayi aiki ko rayuwa tare.
Akwai tunani dadama wajin banbanta irin yanayi mutane,Amma akwai matakai guda hudu dabam dabam.uku daga cikinsu na halayan mutum da kuma bayanin guda hudu daga cikinsu sune:

- DISC- Rinjayayye, albarkachi, halin biyayya, tallafawa.
- Hippocrates- mai saurin hasala, mai halin gaba gadi, mai bakin ciki, mai majina.
- Launuka- ja, mai ruwan kwai, ruwan bula, shudi.

Na zayyana banbanchinsu a ka'ida guda a irin wannan shiri.

A wannan bayanan mai harrufa ne, na zaba inyi anfani da launuka, domin ita ce na fara haduwa dashi a wani bita da kanfanin tafiyarda kimiyya ta hada. Kafin mu cigaba bari in kara da cewa yawan cin mutane sun hada duka guda hudu din, da kuma banbancin karfi a kowane mataki.

- Ja (Rinjayaswa, mai saurin fushi) Burin da za'a cimma:
    - Alama: kai tsaye, kudurtawa, yin gasa, shirye domin daukan kasada, jin dadi zama kan ragama, mai son amsoshi gaba gadi, yanchi daga mallaka, ki zama da buri.
    - Dauki kudiri tawurin gwaji da kuskure, ki darajantu domin sakamako.
    - Idan ke ja ne, kiyi hankali da: cusa ma mutum ra'ayi, kasance da zafi da kunya yawan rook, da kasa sauraro.
    - Cikin sadarwa da ja: kiyi saurin nuna mata muhimancin kudurin domin cimma matsaya, koda a saba maki da wuri.
    - Jajaye suna gwagwarmaya da dan gautaka. Shawarwari: ki ajiye shawaranki tukuna sai in an tambaye ki, koda ki rena wasu, ki shirya ki karbi laifinki, ki kuma roka gafara da sauri.
- Mai ruwan kwai ( Albarkachi, halin gabagadi) Dangantakar da za a cinma:
    - Alamu: mai son cudanya da mutane, mai son wasa, mai son ya chanja a koyaushe, mai jin dadin aiki da jamma'a, masu iya bada labaru da masu horaswa.
    - Daukan kuduri tawurin sauraron ra'ayoyi da kuma zuwa ga kammalawa.

- Idan ke mai launin ruwan kai ne kiyi hankali da: neman ki faranta ma kowa rai, da wargaje shiri, da kuma saurin dauke hankalinki, da kara ma Magana gishiri da kuma mamaya.
- Sadarwa da mai launin ruwan kai: ki taimakesu su zama da hange, yi Magana tawurin damuwan su, ki sa rai ga rudewa, Makara da kuma lokacin kulla dangantaka.
- Masu launin ruwan kai sukan yi gwagwarmaya da yawan Magana da son kai. Shawarwari: ki gajarta sharhin ki, kada ki kara ma Magana gishiri, ki saurari wasu, kiyi kokari tawurin inganta masana'antu.

- Launin (mai halin biyaya, da mai bakin ciki). Labarai da za'a cimma.
  - Alamu: Nema da rike labaru, son koya, shiryawa, bunkasawa, bibiya, jin dadin sabuwar al'ada da kuma tunani.
  - Dauki kudiri tawurin: tattara bayanai da kuma tantanche dukan ra'ayoyi.
  - Idan ke mai launin bula ce, kiyi hankali da: labarai da ake ta nanatawa akai akai, jinkiri wajen daukan kudiri, martaba labara mai makama da dalili bisa na ruhaniya.
  - Tawurin sadarwa da shudi: Ki taimakesu suyi aiki tawurin chanji, kiyi hakuri wajen daukan kudiri, ki saurari manufarsu.
  - Shudi suna gwagwarmaya da bakinciki da kuma nuna kammalawa. Shawarwari: ki kirkiro halin nuna godiya, ki dubi ababu masu kyau, ki zama da jinkai ga kuskuren wasu da kuma kanki, ki gina bangaskiyanki ki gaskanta da Allah.

- Launin Shudi (Mai goyon baya, mai majina) Cimma burin sanin fasalin aiki:
  - Alamu: kebabbe, gargadadde, da bayanin kasashen gabashin duniya, da bin al'adu, ka'idodi da matakai, son bishewa da gargadi.
  - Dauki kudirori tawurin: samun bayanai, da kuma sansance damuwoyi, da kuma samun bayanai na tarihi, da bunkasa dabaru, da kuma ajiye tarihin kome.
  - Idan ke shudiya ce, kiyi hankali da: Yawan mallaka, da rashin wakiltaswa, da kuma rashin lankwasawa da kuma rashin son chanjawa, yawan daukan rubutachen bayanai, abinda aka kafa kuma kan ka'ida.
  - Launin shudi tana gwagwarmaya ba tare da juyayi ba, da kuma tsautawa chanji.

Shawarwari: ki karfafa su suyi sabobin abubuwa, domin su sami abinda suna marmarinsa, su kuma zama da kuzari wajen maganche matsaloli, ki rungumi chanji.
Wani hanya na daban na gane mutane shine wanda ya bayyana tare da iyayen daji, masubi wadanda suka koma daji a karni na uku domin su zo kusa da Allah. Za a iya samun sauran bayanan a yanar gizo.

3. **DANGANTAKA**

A cikin koyaswan yesu ya dauki lokachi yana Magana akan dangantaka. Me yasa ya zama masa da muhimmanchi haka? Dangantakarmu da junan mu ya nuna dangantakar mu da Allah. Ba zamu ce muna kaunar Allah amma muna kin yar'uwan mu ba (1Yohna 2:9) Da aka tambayeshi cewa wanene doka mafi girma, Yesu ya amsa da guda biyu, "kaunachi ubangiji Allahnki da kuma kiyi kaunar makwachiyar ki kamar kanki" (Matta 22:36-39)
Sabon alkawari ya bamu wasu sharuda na danganta kuma: "Kuyi wajuna kirki, kuna tausayi, kuna yafewa juna kamar yadda Allah ya yafe muku tawurinalmasihu". (Afisawa 4:32)
Amma ni ina gaya muku, ku kaunachi magabtanku kuyi wa masu tsananta muku addu'a. (Matta 5:44)
"In kun husata, kada kuyi zunubi, kada ma fushinku ya kai fadiwar rana". (Afisawa 4:26)
Sau da dama a sabon alkawari an umurche mu muyi zaman salama da kauna (Rom,12:18 2korintiyawa 13:11, Ibraniyawa 12:14). Amma mutane suna wuya, wani lokachi ma bashi yiwuwa ne ma baki daya. Yaya zamuyi mu'amala da mutane masu wuyan hali? Tawurin hali, zamu zabi hanya daya daga cikin guda ukun nan, a. gujewa, da b. kai hari ko c. yin salam . Nassin tayi nanachi a kan na karshen.
Mai yiwuwa wannan yanayin kai kadai ne kake fama dashi, ko kuma taimakawa ne shigo tsakanin gungun mutane biyu, tushen ka'idodi iri daya ne. ki fara da komawa baya sai ki auna damuwan. Yaushe ne damuwoyi suke tashi? Ki nemi zare mai sauki sai kiyi addu'a domin hikima da kuma sansacewa.

a. Wannan haduwan yanayin mutane ne ko buri ko sa rai ko kuma dai rashin ganewa ne kawai bias ga rashin sadarwa mai kyau ko kuma rashin sanarwa? Ki dauki lokachi kiyi kina binbini akan wannan yanayin. Ki roki Allah domin hangensa, duba, da sanya lokachi. Idan batun haduwan yanayi ne, sansantawa zai kawo babban dangantaka

mai riba ga kowa, misali Bulus da Barnabas. Idan batun banbanchi daraja ko buri ne, kowannensu zatanemi ubangiji ta kuma sami nufinsa. Idan kuma batun akan muhimman sadarwa ne ko rashin sadarwa, idan muka tattauna  akan batun zai kawo babban fahimta da kuma yarda domin muyi tafiya cikin haske tare (1Yohana 1:7).

b. Wannan shine bakin daga na ruhaniya? Mai yiwuwa ruhun rarabuwa yana kan aiki, ko kuma wasu hare hare na ruhaniya dake kawo ma dukan ku hari, shaitan ya shuka karya a cikin ku domin ya lalata aikin Allah. Idan haka ne, sai ki rushe bangon dake tsakanin ku biyu tawurin bude wani tattaunawa da kuma yin addu'a tare gaba da magabchi (Afisawa 6:12).

c. Wai shin katsewarvdangantakar nan sakamakon zunubi ne, ko zunubinki ko na wasu mutane? Watakila zunubi da ciwo na baya suna rufe hukunchi ko suna tayar da jinki na abinda kin taba fada ko kuma kin taba yi. Menene ke kawo kace nace ko fada tsakaninku? Ba wannan bane cewa, so na kwarai da kuke da shi yana yaki a tsakaninku (Yakubu 4:1)? Kungiyan masu bada salama sun bada ra'ayoyi guda hudu daga litafi da zai taimaka wajen warware gardama.

    i. Ki daukaka Allah ki yarda Allah zai yi anfani da wannan hargitsin da kyau (Romawa 8:28).
    ii. Ki cire gungume dake cikin idonki Mat 7:5, kiyi binbini akan (filibiyawa 4:2-9).

NOTES

iii. Ki maido a hankali. Ki nemi maidowa, ba kayaswa ba (Matta 18:15-18).
iv. Kije ki sulhuntu. Ki gafarta kamar yadda Allah ya gafarta maki (Kolosiyawa 3:12-14) ko wani ya gane aikinsa cikin hargitsin ko babu, Allah ya dokache mu da muyi gafara idan muna bukatan gafara a wurin Allah(Matta 6:15).

idan wannan ne bangaren da kike gwagwarmaya akwai shawarwari a karshen wannan darasi da zaki karanta ya taimake ki.

Domin wani irin yanayin mutum, akwai babban jaraba na kin fuskanta, sai dai asa bege cewa zai wuce. Na yarda da zuciya daya cewa na zama daya daga cikin irin wadannan mutane, a lokachi guda kuma na koya daga abinda ya gudana cewa ba safai damuwa ta kan "wuce ba" sau da dama ta kan dan rufu ne na dan lokachi sai ta bullo kuma, a lokachin da ba a tsammani. Idan damuwar ta cigaba da zuwa cikin tunaninki yau da kullum sai kika iske kanki kina kin wata, kina bukattan ki kawas dashi tawurin addu'a da kuma gaskiya da bangirma cikin Magana da juna, in ya yiwu ma fuska da fuska.

**HADDACEWA:**

- Romawa 12:18- "In mai yiwuwa ne a gareku, kuyi zaman lafiya da kowa".
- Afisawa 4:32- "Kuyi wa juna kirki, kuna tausayi, kuna yafe wa juna kamar yadda Allah ya yafe muku tawurin Allmasihu".

**MABUDIN GASKIYA:**

Ganawa da yanayin banbanchin sadarwa da yanayin mutum yana da inganchi ta wurin gina dangantaka mai karfi da kuma alumma.

**MARTANINKI:**

1. Wani yanayin rayuwa ne kike tunani zai fi gabatar da ke da iyalin ki, idan kina da dama shiga yanar gizo kuma baki taba yin gwaji na yanayin mutuntaka ba, kiyi wannan a www.discpersonalitytesting.com/free-disc-test kyauta.
2. A kowane tattaunawa da zai zo kiyi amfani da dabaran sauraro da kyau ki kuma bayyana ganewa sosai kafin ki amsa. Kada kiyi mamaki idan kin ji abin ba kan gado kamar surutu ne da fari. Kamar yadda yake da wasu

abububuwa, haka nan zai kasance da ma'ana yayinda kin saba da shi. Idan kina bada umurni ga wanda kina aiki tare, ki sa su maimaita abinda suka ji, abin sai ya baki mamaki.

3. Akwai wanda kike gudun ta sabada wani rashin jituwa da ya taba shiga tsakaninku? Kiyi kokari ki bi matakai hudu na yin salama da kuma tunanin jagoranchin Allah game da lokachi.

**DON KARIN KARATUN NAZARI:**


www.peacemaker.net
www.stephenministries.org
www.enneagram.com

Dalilin Abota na Alan Loy McGinnis (McGinnis, 1979)
Maganar Gaskiya cikin Soyayya ta Koch & Haugk (Koch & Haugk, 1992)
Gafara da Manta daga Lewis Smedes (Smedes, 1984)
Gudanar da Rikici Hanyar Allah ta Deborah Smith Pegues (Pegues, 1997)
Personalysis - Fasahar Gudanarwa (Noland, 2015)
Halayen Ƙari - Florence Littauer (Littauer, 1986)
LifeKeys - Kise, Stark, Hirsh (Kise, Stark, & Hirsh, 1996)
Halayen Bakwai Bakwai na Ingantattun Mutane Na Stephen R. Covey (Covey, 1989)

## DARASI NA 9: SHUGABANCHI A INDA ALLAH YA SANYA KI

Wasu daga cikin mu an haife su da matsayin shugabanchi kamar prince Willian na ingila, da kuma kalilan wadanda suke da baiwan shugabanchi (ko dayake wasu sukan saya wannan mukamin) amma ga yawanchin shugabanchi takan bullo ne a hankali, a dabaranche da kuma lura. Don haka ta yaya ne mutum ke fara wannan tafiya na shugabanchi? Ki fara da yin shugabanchi a inda Allah ya ajiyeki. Kamar yadda na fada a baya, ilimin shugabanchi nay a soma ne a sa'anda na sa kaina a aikin ikklisiya da kuma ayyukan dalibai, a karkashin jagoranchi manya a shekaruna da nike tasowa. Darussan shugabanchi da na koya a wadannan shekaran basu zama da daraja ba, yadda zan mayar da martani ga suka da kuma kiyayya, da muhimmanchin gina kungiya, da kuma kafa tushe domin gini mai dorewa. Daya daga cikin muhimman dabarun shugabanchi a rayuwana yazo mini ne a shekaru na ashirin a lokachin hadaddiyar aikina kamar manaja na tuna na taba gaya ma shugabana cewa, "kome da na bukachi in sani shine inyi wannan aiki da na koya a sa'anda nike a gida shekaru goma da yarana biyu maza". Kada ki rena muhinmanchin darussan shugabanchin da kin koya a shekarun kin a tasowa. Yayinda kina kara zama da niyya cikin aikin shugabanchin ki, ina baki shawara ki gwada wadannan ka'idodi hudu:

1. **KI SAMI WAHAYI**
   Menene ki kanyi kokari ki cimma burnish a sa'anda kike shugabanchi? Kina kokarin maganche damuwa, ko tanada hanya ko kuma kwatanche, ko anfani da zarafi ko kuma kokarin cika wani gurbin shugabanchi? Domin karfafa mutane subi, dole ne ki iya sadarwa mai kyau na wahayin da ya karfafa ki kiyi shugabanchi. Mai yiwuwa kina mayar da martani ga motsawa ta

mussaman ne, ko luranki na bukata, ko kuma gayyata daga wani a gwamnati. Musa ya sami wahayi na kubutar da israilawa daga bauta. Cikin rashin sa'a, niyyarsa ta kai shi ga gudu da rayuwansa zuwa cikin daji na tsawon shekaru arbain (40). Kina cikin taron mutane mai kyau idan sanin kin a farko akan shugabanchi bai ci nasara ba, Kada ki fidda rai. Marubuchi John Maxwell ya shawarche mu da mu "fadi ta gaba", muyi koyi daga kurakuran mu.

2. KI SAN KANKI

   Romawa 12:3, ta karfafa mu da cewa kada muyi yawan tunani akanmu fiye da yadda ya kamata. Amma a cikin shugabanchi yana da anfani mu san karfinmu mussaman ma har da rashin karfinmu, domin muyi gini akanshi, sa'anan rashin karfimu kuma mu kudurta yadda zamu yi mu dagasu:

   a. KI San Karfinki: A darasi uku munyi Magana akan baye baye da so na kwarai. Wadannan sune masomi masu kyau domin tunani kan karfinki. Wadanne abubuwa masu kyau ne mutane suke fada akanki a wurin aikinki ko a ikklisiyarki, ko a gida da kuma cikin alluma, mussanman wadanda sun san ki sosai? Kiyi tunani akan abubuwa guda hudu (4) ko biyar (5) da kin fi so kiyi kuma kina tsamani kina yin su da kyau. Idan kinyi tunanin yanayin shugabanchi da a halin yanzu kina tunani akansu, yaya kike bayyana wannan karfin?
   b. Ki San rashin karfinki: Idan kin kasa, menene ainihin dalilin? Wadanne ababa mara kyau ne mutane sukan ce akan ki? Wadanne irin yanayi ne kike da tunanin guje masa in ya yiwu? Kiyi tunani akan abubuwa hudu (4) ko biyar (5) na raunana da suke kalubalantar ki. Yaya zasu rege miki karfin shugabanchi a yanayin da kike a yanzu? Menene zakiyi domin ki maganche wadannan rashin karfin?.
   c. Kisan muradin zuciyarki: yadda kike tunani akan, "shugabanchi a inda Allah ya ajiye ki", Menene muradin ki mafi muhimmanchi? Domin jawo hankulan mutane ko nuna kalma ga wasu? Wane wuri ne fahariya da kwadayi da kyshi da wasu sha'awoyin jiki suka samu zama a cikinki? Ki gaya ma kanki gaskiya da kuma Allah. Musa ya chanja a shekarunsa arbain a jeji, bai sake zama yarima a masar ba, amma ya zama makiyayi, ba mai neman ramako ba kuma, amma ya zama natsatsen mai zaman jeji, maimakon zama mutum "mai girma cikin kalaman sa" (Ayyukan manzani 7:22), ya kwatanta kansa kamar "mara saurin Magana da kuma harshe" (fitowa 4:10). Karfinsa ya

zama rashin karfinsa, amma yanzu a idanmu Allah yana a shirye yayi shugabanchi.

3. **KIJI KIRAN ALLAH**
Manyan shugabanni a litafi mai tsarki kamar su, Ibrahim, Musa, Joshua, Gideon da Dauda, Bitrus, tsohon alkawari da sabon alkawari dukansu suna da hali guda daya zama da kamanni. A wani lokachi a rayuwansu, sunyi "naam" da kiran Allah, babu wani daga cikin su da yayi fice ko kuma ya dace da kiran, yawancin su ma sun dubi kansu kamar basu chanchanci shugabanchin ba, amma duk da haka suna shirye suyi biyaya da kiran Allah. Zamu ji bamu isa ba idan Allah ya yi mana Magana yadda yayi ma Musa, "menene ke hannunki"? (fitowa 4:2). Tambayan ita ce ko zamu yi nufin mu zaba mu fito cikin bangaskiya da biyaya muyi anfani da abinda muke dashi dominsa kamar karamin yaro a lokachin ina da wani waka da nike jin dadi kamar haka "shangar yana da Dauda yana da majejjewa, Tabitha tana da allura, Rahab tana da zare, Samson yana da mummuke, Haruna yana da sanda, Maryamu tana da man kanshi kuma dukansu Allah yayi anfani da su". Menene ke hannunki?

4. **KI GINA KUNGIYA**
Daya daga cikin nawayan shugabanchi a farko shine a gina kungiya wanda zasuyi wannan tafiyan tare dake. Yaya kike zabansu? Ki nemi mutane masu fadin gaskiya masu daraja da zasu fadi gaskiya kome dacinta, mutanen da sun sami wannan wahayi kuma suna da marmarin yazo ga wucewa, mutane da suna da hikiman da zasu gan ramuka da ke baki gani ba, mutanen da karfin su yaya a wajen rashin karfinki, mutanen da kina a shirye ki basu amana domin kin yarda da hukunchin su da kuma aminchinsu, mutanen da

NOTES

kina a shirye ki basu ikon yin maki gyara a duk sa'anda kin kauche, mutanenda zaki bayyana musu zuciyanki a sake ki kuma san cewa zasu kaunache ki duk da kasawanki. Ba lalle ne wadanda ke kusa dake su zama da yawa ba. Bayan addu'an dukan dare, Yesu ya zabi mutun goma sha-biyu cikin wadanda suke binsa, amma yafi kusa da mutum uku (3) kawai.musa ya zabi kaninsa ne kawai, domin ya sanshi sosa,amma Allah ya zabi shi kamar abokin tafiya.ki gina kungiyan ki a hankali cikin addu'a ki mika kai ga kauna,bunkasawa da kuma bauta musu,ba yin anfani dasu kawai domin cimma manufarki ba. Ginin kungiya a hankali yana farawa da dangantakar koyo na daya da daya, da jin zukatan jamma'a da labarum rayuwa, sa anan a hankali a gina yarda da kuma gabagadi.

Ina ne Allah ya ajiyeki? Ya baki wahayi da yake so ki cika? Kin sami lokachi a gabansa kin tantance karfinki da rashin karfinki kina jarraba muradin zuciyarki? Ya kiraki ya tabbatar maki cewa yanzu ne lokachi ki amsa kiransa? Ko ya sanya masu rikon amana cikin shugabanchir ki a albarkacinki?

**HADDACEWA:**

- Romawa 12;3-8 Albarkachin alherin da akayi mini ina yi wa kowanenku gargadi kada ya dauki kansa fiye da yadda ya kamata,sai dai ya san kansa, gwargwadon bangaskiyan da Allah ya bashi 4.wato kamar yadda gabobi da yawa suke harhade a jiki daya,gabobin nan kuwa ba aiki iri daya suke yi ba, 5.haka kuma, ko dayake muna da yawa, jiki daya muke hade da Almasihu kowananenmu gabar danuwansa ne 6.Da yake muna da baiwa iri iri,gwargwadon alherin da aka yi mana,to sai muyi amfani da su.in ta annabchi che,sai muyi anfani da ita gwargwadon bangaskiyan mu, 7.in ta hidima ce,wajen hidimar mu,mai koyas da maganar Allah kuwa wajen koyaswan sa 8.mai karfafa zuciya kwa wajen karfafawarsa,mai yin gudummawa kuwa, ya bayas hannu sake,shugaba yayi shugabanchisa da hikima, mai yin aikin tausayi, yayi shi da fara,a.

- 1 korintiyawa 12:4-11 [4] To akwai baiwa iri iri amma ruhu daya ne [5]. Akwai fanni iri iri na ibada amma ubangiji daya ne. [6].Akwai kuma aiki iri iri, amma Allah daya yake iza kowa ga yin kowannensu. [7]. Anyiwa kowanne baiwa da wani budi na ruhu, don kyautatawa duka. [8]. Wani anyi masa baiwa da koyar da hikima ta wurin ruhu, wani kuma da koyar da sani ta wurin wannan ruhu, [9].wani kuma anyi masa baiwa da bangaskiya tawurin ruhun nan, wani kuma

baiwar warkaswa tawurin ruhun nan, 10. Wani kuma mu,ajizai wani kuma annabchi wani kuma baiwar rarrabe ruhu da aljani  wani kuma iya harshe iri iri, wani kuma fassara harsuna.11. Dukan wadannan ruhu daya ne yake iza su ,yake kuma rarrabawa ko wannensu yadda ya nufa.

**MABUDIN GASKIYA:**

Idan ikn yarda Allah na kiranki domin shugabanchi, ki fara da zaman aminchi,da mika kai, da kuma bin shugaba mai kyau da kuma wanda za ayi koyi dashi, kina bada labaru, kina kuma rarraba nawayya da iko.saanan a lokuta da dama shugabachi zata biyo baya don kanta.

**MARTANIN KI:**

1.ki lura da shugabaninki awurin aiki,ko a ikklisiya ko a allamuranki da kuma iyalinki,domin ganin wanda zata bada dokan bangirma da soyayya na wadanda ke kawaye dasu.Idan ba irin wannan a tsakaninku,sai ki fara karatun tarihin shugabani masu kyau wanda kinyi shaawansu.ki zayyana abubuwan da kin koya daga wadannan mutani.

2.Kiyi waiwaye akan abin da kika sani a gida kamar shugaba,ko a ikklisiya ko a aiki ka cikin allama ,ko cikin daginki.zakiyi mamaki  ganin irin shugabanchin da kike da shin.menene kin koya a wadannan koyaswa wadanda kikayi nasara da kuma wadanda kin fadi?

3.Ki auna yanayin shugabanchin ki a wannan matakai:[1=kasa, 5=Bisa].

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| Yardajje | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Mai kyau | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Natsattse | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Mai sauraro da kyau | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Budadden zuciya | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Mai juyayi | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Mai hikima | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Kirkiro dabaru | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Mai hange | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Mai saukintankwara | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Motsa wasu | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| Sanya ya zama da kyau, kudiri akan lokaci. | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |

4.Zaki iya bincikan kanki tawurin gaya ma abokiyanki ku tattauna akan yanayinki(ko kuma ki tambayi wasu domin su cika maki bisa ga rayuwanki). A wuraren da kun kai uku ne kaiwai ko kuma kasa da haka, me zaki yi domin ki tashi bisa domin ya chanja rashin karfinki da wani a kunkiyaki?

**DON KARIN KARATUN NAZARI:**

Nufin Jagoranci na Marvin Bower (Bower, 1997)

Jagora daga Zuciya na Jack Kahl (Kahl & Donelan, 2004)

## DARASI NA 10 :AIKIN HADIN KAI-SHINE MABUDI

Yayin da muke bincikan nassi da kuma halayan Allah,ba muda wani zabi amma mungane cewa Allah bashi da raayi wajen bada gabatan mu domin jin dadi na dan karamin lokachi na yanzu.can baya a kwanakin Ibrahim yana da shiri bayananne domin sadar da kaunarsa ga duniya.Ta kunshe alkawari da mutuum daya wanda zai sadar da bangaskiyan sag a iyalinsa kuma zuriyarsa zasu kai duniya.

(farawa 18:18) Ya zabi dan kankanin kasa da kuma mutane su zama nasa.Yesu ma ya bi wannan tsarin.Ya fara hidmarsa a wani kauyi mai nisa daga harabar urshalima masu addini tare da yawanci masu kamun kifi,masu karban haraji da kuma wadanda aka kori su daga alluma.yaya ya bunkasa kungiyan da ta chanja duniya har yanzu kuma tana shafan shugabanni da mabiyansa a yau?

## 1 CIKIN ADDU'A KI ZABI YAN KUNGIYA.

A darasin mu da ta wuce na bada shawara cewa ki fara neman yan kungiyan ki ta wurin lura da halayansu.su mutane ne da zaki yarda dasu?masu gaskiya ne,masu aiki tukuru ne,kuma a shirye ayi musu gyara,suna kuma kasanciwa su koya,suna kuma da juyani cikin dangantakarsu da Allah,suna kuma murna cikin ruhu,cike da gaskiya komin dacinsa,masu tallafawa iyalai kirki ga duk wanda suka gani,balagaggu cikin ruhaniya,masu yafewa ,masu rahoto mai kyau cikin aikinsu, masu aikata alheri da kuma kauna?kamar abubuwanda aka zayyana anan sunyi yawa kuma zasu zama da wuyan yiwuwa.Burin ba wai ki zama cikakkiya a kowane bani,sia dai bayyana yada kike zai taimaki ki san inda yaki bukatan a

kauda fuska domin kawas da yanayin daga inda zasu iya fadiwa.kiyi yadda zaki san su.labarinsu,karfinsu darashin karfinsu,abinda suke so da abinda ba su so,sanaarsu da abinda suke shaawa,yadda suke sadarwa,da kuma yanayin haushinsu,basu a wurin jarrabawa daya,ama akan cokachi yayinda dangantakarki da kowannansu yana girma.

Yesu ya zanta da almajiransa game da rai a hanya,yana tafiya,yana ci,yana barchi tare dasu,a dukan lokachi yana daukan daman kowane lokacin koyaswa domin ya kalubalance su suyi girma su kuma bunkasa kamar mutane samaria,kogin galili,ko abikin rijiya a ya kuma koya musu yadda zasu zurfafa dangantakar su da abansu na sama tawurin addu’a da kuma sanin rubutacheyar maganar Allah cikin addu’a ki nemi mutanen da martabansu da karfinsu,da rashin karfinsu,da gwanintansu ya sha banban da naki.wannan zai bukaci niyya.mukan jarabtu mu zabi masu Magana da kuma tunanin da yin kome kamar mu,wadanda suke cin moraya ayyuka iri daya masu irin aladu daya da nasu.amma muna gina wata kungiya,wato icke da yake bukatan banbantawa (Afisawa 4:16).

Mai yiwuwa ba zaki iya samun zarafin da za ki gina naki kungiya ba.mai yiwuwa kuma gaji wani kungiya na da wata ta kafa, amma kuma mafarin wurin daya ne wato dangantaka na daya da daya.

Luka:12:16 ta gaya mana cewa yesu yayi addu’a dukan dare domin zaban wadanda zasu taimaka masa aiki.bashaka yana lura dasu a cikin jama’a da suke sauraronsa,amma yana bukatan hikima Allah da kuma manufansa cikin zabinsa na karshe. Kada ki rege muhinmanci wannan kuduri wadannan ne zaki ni tafiyan shugabanci tare.wadanda Allah ya zaba zasu iya baki mamaki.ina tunani ko yesu yayi mamaki da zaben yahuda da Allah yayi,in haka ne wani bangaskiya ne ya sanya har aka danka masa ragaman jakan kudi?

## 2. HADA KUNGIYA

Mudin kayan ginin kungiyar ka suna nan a kasa asaurin aikin sanin tsayayyar jiki mai manufa mai kyau ya soma wannan zai fara bukachi ke kamar shugaban ki iya sanya wannin ki abayyane da Allah ya baki.kina sadar da wannan wahayi a hanyan da kowa yana da hange iri daya na inganchi da kalubalachi.baki son yan kungiyaki su zama kamar makafi wadanda kowannansu ya bayyana giwa gimshiki ko igiya ko reshen itace, ko fanka, ko bango ko kuma bututun ruwa, bias ga yadda suke ganin shi. Yanayin da za’a bayyana wahayin da sauki hakanan ne yan kungiyanki zasu fi samunshi da saukin ganewa, hakanan kuma za’a samu saukin hada kansu wajen cimma wannan manufa. Daukan wahayin da sauki ba

karamar nauyi bane kuma ba za’a dauketa da wasa ba. Bayan kin bayyana musu wahayin ki, ki tambayesu abinda wannan yake nufi a garesu kada ki dauka kamar sun gane.

Mataki na biyu shine ki bayyana musu yadda ku kamar kungiya zaku iya cinma wannan wahayi. Sai in Allah ya rigaya ya bayyana shirinsa gareki. Zan baku wani misali, mai yiwuwa wahayinki zai iya zama allama ne na mata masu kauna, karfafawa da kuma mara ma juna baya wajen tafiya da Allah da kuma yadda zai zama tawurin yin binciken maganan Allah da kuma addu’an tarayya da hadaddiyar sujada da kuma bautan juna.

3. YI WA JUNA HIDIMA

Ba zamuyi kama da Yesu bai dan bamu yin tafiya tare kamar jiki daya, cikin hadin kai, kauna na karfafa juna (Yohana 17:21).

Nazo ga ganewa cewa gasa a tsakanin yan kungiya zai iya kawo sakamako na karamin lokachi amma kuma a karshe zai kawo kishi, da fahariya, da rashin yarda da zato a tsakanin yan kungiya, yana dauke hankalinsu daga wannan wahayin kungiyan, maimakon haka, ki karfafa yan kungiya domin goyon baya da karfafa juna, a taimaki wadanda suna gwagwarmaya, a yawaita kalma, hadin kai da koyo tare, idan kina da kananan tattaruwan mutane a misali, sai wata gungu tana kokari amma wata kuma tana rawa, ki karfafa shugaban wannan kungiya mai kokari domin ta sadu da shugaban kungiyan da tana rawa domin su tattauna tare. Wani dabara kuma shine a rika zaman kungiyan akai akai inda shugabanin zasu rika tattaunawa akan cigaban su da kuma rashin cigabansu sa’anan su duba tare abubuwanda suke fuskanta. Maimakon yin gasa da juna, ki karfafasu su sanya burinsu ya zama wadanda suna da alaka da kungiyan ne gaba daya.

NOTES

Kwatancin bangirma da kaunar juna cikin aiki, da Magana da tunani. Yesu yakan samu lokachi domin mutane a kullayomi, mussaman masu bakin ciki, masu ciwo ko ciwon zuciya. Ya samu mawuyachin aikin bishara da zai aiwatar cikin shekaru uku na hidimarsa, amma bai dauke shi da garaje ko da hanzari ba. Asirin it ace bangaskiya a kullum da kuma naciya da biyaya cike da bangaskiya ga ubansa. (Yohana 5:19).

**4. KULA DA KUNGIYA MAI LAFIYA**

a. Ki karfafa koyo da girman mutane. Daya daga cikin abubuwa masu muhinmanchi ke kamar shugaba zaki yi shine ki karfafa girman mutuum da kuma bunkasa membobin kungiyan ki. Ki taimakesu su gane kiran Allah a rayuwan su yana bukatan kin una masu rayuwanki, wanda daga baya ta kunshi halin wuyar tsarewa da gaskiya da kuma kaskanchi a gefen ki. Kiyi musu addu'a da gaske, ki saurari begensu da maffalkansu, sai kiyi duk abinda za ki iya yi domin ki taimakesu zama abinda Allah ya kirasu su zama. Idan sun zama masur ikon amana da kuma wadanda za'a dogara garesu, sai ki danka musu nawayan da zai bayyana halinsu. Yesu ya aiki almajirai sabain da biyu zuwa garuruwan da zai je da gargadi ta mussaman akan abinda zasu dauka da abinda zasu fada da kuma abinda zasu yi. Suna da cikakken shiri da zasu fita da kansu suna warkasda marasa lafiya suna kuma wa'azin bishara? Lalle basu da wannan shiri na ruhaniya, kamar yadda abin yazo ga bayyanuwa daga baya, anma da karfin Allah, sun cinma burin da Allah ya aiko su suyi, sun ma yi mamaki akan sakamakon abinda ya biyo baya (Luka 10:1-20).
Akwai jaraban neman ajiyesu "a karkashin fikafikanki" bayan kin horas dasu sun zama gogaggu daga cikin kungiyanki. Ki tsauta ma wannan ji, ki sake su suyi aikin da Allah ya kira su ya kuma iza su suyi, ki bada gaskiya ga Allah domin ya sake tada wasu domin su cike gurbin da wadancan suka bari. Ba tareda wannan ba, kungiyan ki zai zama kamar matasa masu tasowa da suke a shirye babu wurin zuwa.

b. Ki fadada manufan taron kungiya.
Tarrukan kungiya ya kamata ya zama da manufa, da nuna kauna da kuma koyon zarafofi ga duka, kafin taron, ki shirya kawunan Magana da za'a tattauna akansu, ku fara kowane taro da addu'a da kuma rufewa da addu'a, ki shirya tattaunawa mai muhinmanchi a farkon taro domin a samu cikakken lokachin tattaunawa da amsa tambayoyi. Yi kokari ki'manta lokacin da kowane kan Magana za ci domin a iya ajiye kayadadden

lokacin da za'ayi a wannan taro, idan yana da muhimmanchi ga mahalarta taron. Idan kowane kungiya zata bada rahoto, sai a bada tsawon lokachi da kowane rahoto zai dauka, za'a kuma bada sharruda ga kowane kungiya game da abinda rahoto zai dauka. Wata kila ma abubuwanda aka tattauna a taron da kuma cikakken bayani a rahoton a rubuche ne za'a mika. Lokachin taron kungiya yana da muhimmanchi, yi anfani dashi da hikima da motsa zuciya, da chanjawan manufa da kuma nachewa da sadar muhimman labaru ga kowa. Kalaman gyara ga mutane dole a rike su da lura. Taruwan kungiya zai sake zama da muhimmanci gareki kamar shugaba domin ki sansance matsalolin da ke akwai tsakanin membobin kungiyan ki.

Ki nemi wani kungiya da ba membobin kungiyan ki sai kiyi abubuwan da zai karfafa membobin kungiyan ki su bunkasa dangantaka da wadanda suke da ra'ayi daban da nasu.

c. Ku sami lokachi tare.

   Ku ji dadin zama tare, kuma rayuwa tare a lokachin da kuka samu.

   Ki roki Allah ya nuna maki hanya da zaki yi wannan, kuma tattaunawa akan nawayyan gida, zuwa shan iska tare. A lokachin ne ake kera dangantaka.

   Zumunta da juna wani muhimmin hanya ne na gina dangantakan kungiya, ba bata lokachi ba don dai babu wata manufa da ta cika. Ki koya kiyi dariya ko kuka tare a yayinda kike sauraron damuwoyin junanku.

d. Ki tsaya a shirye.

   Ku dubi "kananan yanyawa da suke bata gona" wadannan kananan abubuwan masu tada hankali da sukan yi girma sossai a lokachinsu (w.wakoki 2:15). Ki rike su da farko da addu'a da kuma hikima. Sanya lokachin da za'a yi musu Magana yana da hatsari, kamar yadda za'a kusance su. "fadakarwar da mutumin da ya gogu da alamuran duniya yayi ga wanda yake da niyya ya kasa kunne, tamaninta yafi na zoben zinariya, ko kayan ado da aka yi da zinariya tsantsa". (Misalai 25:12).

   Ko magananki zai bata ma wata rai ko ya zama kamar adon zinariya zai danganta ne ga lokachi. Litafin misalai yana cike da kalaman hikima masu daraja. Ki dauki lokachi kiyi binbini akai guda daya ko biyu a kullum, zaki gina wajen tara ruwa mai zurfi wanda zaki rika dibawa a ciki.

**5. GUJE MA**

Daya daga cikin babban rauni na hidima shine ciwon zuciya da kuma na ruhaniya. Bukatan suna da yawa, bukatun mutane dukan a cinyewa. Idan bakiyi lura ba zaki fara ji kamar nauyin duniya duka yana a kafadar ki, idan kuma kin dena rike numfashinki, zai juyo maki. Wannan shine karyan magabchi da fahariya. Aikin na Allah ne mutanen kuma nasa ne, ban aka bane. Ki gwada rayuwan Yesu. Akwai lokatai da Yesu ya janye jiki da almajiransa, akwai kuma lokacinda jama'a sun rokeshi ya tsaya amma ya tafi abinsa. Idan akwai wani da yaji zafi na lokachi, zai zama Yesu ne, wanda ya sami shekaru uku domin ya horas ya kuma tanada ma mutane goma sha biyu kayan aiki domin chanja duniya duka. Duk da haka ya dauki lokachi ya shirya, ya huta, yayi addu'a yayi tunani, ya kuma inganta dangantaka na mutuum daya da daya. Allah bashi da wani shirin mara masa baya.

**HADDACEWA**

- Yohana 13:35- tawurin haka kowa zai sani ku almajiraina ne, in dai kuna kaunnar juna.
- Philibiyawa 2:2-4- to albarkacinsu ku cikasa farin cikina da zamanku lafiya da juna, kuna kaunar juna, nufinku daya, ra'ayinku daya, kada kuyi komi da son kai ko girman kai, sai dai da tawali'u kowa yana maida danuwansa yafishi kowanenku kada ya kiya da harkar kansa kcuwai, sai dai ya kula harda ta dan uwansa ma.

**MABUDIN GASKIYA:**

Gina kungiya wato "jiki" na mutane daban daban da hadaddiyar manufa da kaunar juna shine asalin shugabanchi nag aske.

**MARTANIN KI:**

1. Idan zaki dauki kungiya mai manufa domin cimma burinki, wane zaki zaba kuma don me zaki zabeshi?.
2. Wadanne manyan kalubale ne kika gani a kungiyan da kike a yanzu? Menene karfin kungiyan da rashin karfinta? Zaki iya ganin kamar wadannan tambayoyi ne masu wuya, amma suna da muhimmanchi ga shugabani su amsa.

**DON KARIN KARATUN NAZARI:**

Good to Great na Jim Collins (Collins, 2001)

Rashin Ayyukan Ƙungiya Biyar na Patrick Lencioni (Lencioni, 2002)

Ladabi na biyar na Peter Senge (Senge, 2006)

## DARASI NA 11: AN KIRA DOMIN A BI

"Biyo ni". A bakin kogin galili, Yesu ya fara anfani da wannan kalamomin ga wasu masu kamun kifi su biyu da suna gyara tarun su, martanin su a lokachin shine sun zubasda tarunsu suka bishi. Har yau yana wannan Magana ga almajiransa. "Kada kaji tsoro, na fanshe ku, na kira ku da sunanku, ku nawa ne" (Ishaya 43:1). Wannan it ace ainihin kiranka na rayuwa, yin tafiya da mahallichin duniya duka wanda yana kula da ke da dukan abinda yake kewaye dake, yana kuma sauraron zuciyarki, yana kuma sane da yawan suman kanki, yana kuma tanada ta'aziya a kullum, da hikima da karfafawa (Luka 12:7).

Amma kuma ya sake ba kowannen mu kira na biyu mafi muhimmanchi domin dalilin mulkin sama, kira da akayi ma kowa bias ga baiwansa da yanayinsa da kuma halinda yake ciki. Ga wasu, kiran yana da karfi kuma nawayyar tana da girma sosai, tana bukata dukan iyakan rayuwan ki ne kafin ya cika. Wani mai suna William Wilberforce wanda ya maganche batun sayan bayi a kasar Ingila ya sami irin wannan kiran na rayuwa, kamar yadda manzo Bulus ya samu. Ganewa nay a zama cewa ga yawancin mata a wannan kira na biyu ya banbanta a lokatai da dama a rayuwan mu. Ni dai a gareni, yanayin rayuwa ya zama da kyau kamar dalibi ko matan aure ko mama ko mai ayyuka da yawa ko hidima da kuma murabus aiki. A kowane yanayi, an kirani inzo in bi Yesu, amma wurarenda ya kaini, da kuma ayyukan da ya bani kayan yinsu sun banbanta. Abinda nazo ga koya shine a kowane rana a kowane lokachi, ainihin aikina shine in dauki giciyena in bishi (Markus 8:34).

Ba zan rudi kaina in ce inayi rayuwana mai kyau ina kuma jin kiransa a fili ina kuma tafiya bisa sawun kafansa ba. A shekaruna na kurchiya ni mai farantama

mutane rai ne, ina tunanin cewa idan na faranta ma mutane rai ina faranta mashi rai kenan. Amma wannan ya zama mani da wuya sa'anda faranta ma wani rai yana bata ma wasu rai. Sa'anda nazo ga ganewa cewa ina bukata inyi rayuwa na ne kawai a gaban mai sauraro daya wato Allah.

1. **MENENE KIRA?.**

Mutane suna Magana akan wadanda suke da wani kira ko sana'a amma bazasu yarda ko akwai kira ba, amma dai dole akwai mai kira. Mu kamar masubi muna da daraja a wannan, cikin "kira", wani mai suna *OS Guiness* ya fassara kahyan kira kamar "Gaskiyan da Allah ya kira mu zuwa gareshi da kudurtawa cewa duk abinda muke, da duk abinda mukeyi, da duk abinda muke dashi yana ajiye tare da addu'a da mussamman. Wannan yana nufin cewa ko ina sarrafa naura mai kwakwalwa a wurin aiki, ko ina ta'aziyantadda yaro marar lafiya a gida, ko ina ba mace mai bakin ciki shawara a ikklisiya, ko kuma ina fita yawon shakatawa da mai gidana, ina yi ma wanda ya kirani ne. " **kome kuke yi a game da Magana ko aikatawa, kayi duka da sunan Ubangiji Yesu, kuna gode wa Allah uba tawurinsa" (kol 3:17).** Idan rudani yayi mani yawa da ba zan tafi tare dashi ba, ba zani ba. Idan na fadi wani abu da bai kamata in fad aba, na san cewa ya ji ni, ina bukatan gafartawa nan da nan. Yace ba zai taba rabuwa dani ba, don haka na sani yana gani yana kuma sane da duk abinda nace da abinda nayi da abinda nike tunani.

Yawancin mutane suna tsaye akan abinda aka fada cewa kira zuwa hidima babban kira ne fiye da wanda mutum ya karba na shiga cikin sana'a. A rayuwana na samu haduwa da irin wadannan kiran, kamar uwa mai yaro biyu a makaranta na farko dake zaman gida, naji kiran Allah da in koma cikin sana'a. Tare da yardan maigidana, nabi wannan shawaran sai cikin wata guda, bayan na dena zuwa aiki na tsawon shekaru goma sai na dawo aiki iri daya a kanfanin da na yi aikin kuma wurin da na bari na tsawon shekaru goma. Cikin watanni uku kanfanin bata cigaba da yin hay aba, amma Allah yayi Magana da zuciyata a lokachin da ya kamata. Na zauna a wurin na tsawon shekaru goma sha takwas, sa'annan da cikakkan fahimta na san cewa lokachin tafiyata yayi.

Tawurin **Titus 2:3-4** na san Allah yana kirana domin inyi ma mata hidima, cikin wata shida an sayar da kanfani na, sai aka rufe offishin daga baya. Daganan sai na zama shugaban mata a ikklisiya na, daga sani na zan iya tabbatar maku cewa kira zuwa hidima muryanshi baifi kara ko ruhaniya

ko muhimmanchi fiye da kira zuwa aiki ba, batun shine ko muna sauraro da kuma biyaya da kiransa.

Yaya zaki gani kiranki? Amsan mai sauki ne shine ki sami dangantaka da mai kiran, bayan wannan sai hakuri da biyayya, ki roke shi ya bayyana maki ko wacece ke, yaya kike da daraja, kuma don me kike da daraja, tambaya ne wanda yake son amsawa.

## 2. ABUBUWAN DAKE HANA BIN YESU

Ga wasu, batun ba wai sanin abinda yake so kiyi bane, amma yinshi, me ke hana ki bin Yesu a sa'anda yayi kira?

a. Wasu suna cewa abinda yake ce mini inyi bashi da wani manufa, ba kuma makama mai dorewa, Allah Allah ne na ka'ida, yana gani fiye da hangen duniya, abinda ba zai zama da wani alfani garemu ba yanzu shine yakan zama sakamakon wahayin mu na karamin lokachi, Allah yace ma Ibrahim ya bar kasarsa zuwa Kasarda bai ma sani ba tukuna(Farawa 12:1). Ya umurchi Gideon ya aika da dubban sojoji gida domin yayi anfani da sojoji dari uku kawai wajen yakan dubban sojojin abokan gaba (Alkalawa 7:1-25). Yesu ya bar li'azaru yamutu, domin ya tada shi a rana ta uku(Yohana 11:1-43). Allah ya zabi mutumin da yake tsananta ma masubi ya jagoranchi kungiyan bishara zuwa ga alummaI (Ayyukan manzana 9:15). Yakan zabi raunana bam ai karfi ba domin ya tabbatar da manufarsa (1Kor 1:27). A karshe duka batun bangaskiya ne. na gaskanta cewa shine yake kirana, kuma shi wanda ya fara abu mai kyau a cikina zai kawo shi ga chikawa a ranan Yesu Kristi (Flibiyawa 1:6).

b. Wasu sun ce abinda yake so inyi yana da wahala sosai, suna da gaskiya akwai tamani na zama almajirin Yesu, a lokachi mai sauki zai baki daman yin zabi a naki hanyan. A mawuyacin lokachi zai iya sa ki rasa kome har ranki ma, amma a karshe madawamin lada mai tamani zai zama naki (Ibraniyawa 11:6).

c. Yaya zan iya sani cewa abinda nike tunani sako ne daga wurin Allah ko kuma nawa tunani ne kawai? Gwadawa na daya shine wahayin Allah zai daukaka shi ya kuma fadada mulkinsa, dabarun kanki zai iya daukaka kanki (Ibraniyawa 11).

d. Ban san yadda zan ji in kuma sansance muryam Allah ba. Ba zai fi mani sauki in bar yanayi ya kudurta mani abinda zanyi ba? Cikin

Yohana 10:27 Yesu yace, “Tumaki nawa sukan saurari muryata, na san su, suna kuma bina” idan ke tumakinsa ne zaki ji muryarsa. Tambayan itace ko zaki iya gane muryarsa da sauran muryoyi da suke ta kokuwa neman hankalinki, kamar yadda jariri yakan koya ya gane muryar mamanshi domin ta saba da jin muryan, hakanan zamu koya mu gane muryan ubanmu tawurin samun lokachi dashi, da karanta maganarsa domin mu gane halinsa, mu kuma inganta dangantakarmu dashi. Sa’anda muka ji muryar dake gaba da nashi sai mu san cewa ba daga wurinsa bane “11Gama na san irin shirin da na yi muku, ni Ubangiji na faɗa. Shirin alheri, ba na mugunta ba. Zan ba ku gabata da sa zuciya. 12Sa'an nan za ku yi kira a gare ni, ku yi addu'a a wurina, zan kuwa ji ku. 13Za ku neme ni ku same ni, idan kun neme ni da zuciya ɗaya. 14Za ku same ni, ni Ubangiji na faɗa, zan mayar muku da arzikinku, in tattaro ku daga cikin dukan al'ummai da dukan wurare inda na kora ku, ni Ubangiji na faɗa, zan komo da ku a wurin da na sa a kwashe ku a kai ku zaman talala” (Irmiya 29:11-14).
Na bada gaskiya cewa kiran Allah baya kuskure kuma ba za ayi watsi dashi ba, ki rike alkawarinsaa ke tumakinsa ne zaki ji muryarsa.

**3. AMSA KIRAM**

a. Bin Yesu zabi ne na dukan rayuwa da kuma kudiri na kullum. Kowane Safiya sai nayi zabi in bishi a wannan rana,

NOTES

NOTES

inaso in gode masa domin ba wata kalubale da zan fuskanta a wannan rana da bai rigaya ya kintsa ni in fuskanche shi ba, kuma na rokeshi ya taimakeni in kasance da samun kasancewarsa a dukan wannan rana. Sai in bada gaskiya gareshi domin ya bayyana nufinsa yayinda rana na wucewa.

b. Bin kiran Yesu da kuma anfani da baiwan da ya bani domin manufan mulkin sama baya guma ni. Aikin da kansa zai iya zama karama ce da rashin tunani, amma muhimancinsa zai zo domin ina yi masa. “23Kome za ku yi, ku yi shi da himma kuna bauta wa Ubangiji ne, ba mutum ba, 24da yake kun sani Ubangiji zai ba ku gādo sakamakonku. Ubangiji Almasihu fa kuke bauta wa! (Kolosiyawa 3:23-24). An tunasheni maganan dan uwa *Lawrence* wanda ya koya “sabawa da kasancewar Allah” yayinda take wanke kwanoni, ko aikin da muna yi yana jawo wani mutane zuwa Kristi ko babu, idan ana yin haka cikin biyayya da shi, duka zasu karbi ladansa, aikin bashi da tasiri.

c. Yin anfani da lokachi a bin Yesu yana da muhimanchi sa’anda Yesu ya kira mu mubi zai iya bamu sharuda da zamu bi nan da nan ko kuma ya shirya zukatan mu domin abinda zai sa muyi nan gaba. Kiyi lura kada kiyi tunani cewa abinda yana so kiyi yanzu ne, amma ki jira lokachinsa kafin ki shiga cikin aiki (Yohana 7:3-10). Sau da dama nikan yi tunani cewa da ina cikin yayan isra’ila cikin jeji suna bin umudin wuta. Wannan yana nan a bayyane kuma da sauki, amma kuma nikan tunashe kaina cewa ina da ruhu mai tsarki a cikin wanda yake bishe ni.

d. Bin Yesu ba yana nufin lalle ne sai mun biya bukatun wadanda ke kewaye damu bai dan mun gaskanta cewa dole ne mu biya kowane bukata na mutane, zamu iske kanmu cikin matsanacin rashi, zamu kuma sadu da karin bukatun mutane. Amma idan muka amsa kiranmu, zamu iya aiwatar da abinda Allah ya kira mu, mu kuma yarda dashi domin ya kira wasu domin su

biya bukatun wadanda mu bamu iya mun kai ba, idan mun tsaya akan biyan bukatun mutane ne, zamu gaji a sa'anda mutane suna nuna rashin godiya ko rashin kula akan abinda muke basu.

e. Sa'anda Yesu ya kiramu mubishi, zai iya bamu wahayi bayananne na inda zamuje ko kuma babu, amma zai gaya mana abinda zamu yi nan gaba. Ibrahim bai san inda zashi ba, amma ya san inda ya fara tafiya, amma kuma an ba Nuhu kayadadden umurni, me yasa ya zama haka? Shi Allah ne. "Ubangiji ya ce, "Tunanina ba kamar irin naku ba ne, Al'amurana kuma dabam suke da naku. Kamar yadda sammai suke can nesa da ƙasa, Haka al'amurana da tunanina suke nesa da naku". (Ishaya 55:8-9).

f. Idan Yesu yayi kira sai mu zama da murna domin samun zarafin yin aikinsa. Zai iya zaba yayi aikinsa shi kadai ba tare damuba, maimakon haka yayi mu mu zama abokan zama.

g. Bin kiran sa mika kaine na dukan rayuwa, yanayi da allamura har ma da buri zasu iya chanjawa a wani lokachi amma babu murabus daga kira da yayi mana, mama *Teresa* tana koyaswa a babban makaranta a Calcutta sa'anda ta kamu da cutan tarin fuka sai aka aika da ita a kasar *Darjeeling* domin hutu da farfadowa. A hanyar ta na zuwa can a cikin jirgin kasa, taji kira cewa tayi "aiki da talakawa da suke a cikin su". Ta kwatanta wannan kira kamar "doka". Wannan doka ne yasa ta fuskanchi aiki da talakawa har iyakan rayuwanta. (www.ewtn.com - Shekarun Farko).

## 4. JARABOBIN KIRA

a. Girman kai: Wasu da sun taba samun kiran Allah sun dauka cewa Allah ya zabe su ne domin sun fi sauran ruhaniya, ko tsarki, ko adalchi fiye da sauran, amma bulus yace, "Amma Allah ya zaɓi abin da yake wauta a duniya, domin ya kunyata masu hikima. Allah ya zaɓi abin da ke rarrauna a duniya, domin ya kunyata ƙaƙƙarfa". Sai Bulus ya zaba da farinciki ya zama rarrauna, "….. domin ikon Almasihu ya zauna tare da ni"(1kor 1:27, 2kor 12:9). Fahariya mumunan zunubi ne, yana gayyatar lalacewa da hali ga Allah (misalai 16:18, 1bitrus 5:5).

b. Hassada: sa'anda mun ga wani yana farin ciki ko yana samun cigaba fiye da mu, mussaman wadanda muke da irin kira daya da baiwa daya, wannan yakan sa kiyi bakin ciki? Idan haka ne,

hassada ta shigo, misalai 14:30 ta gargade mu cewa "kishi yana kama da ciwon da yake cin kasha".

c. Hadama: kina yin abinda kike yi domin an kira ki kiyishi ne, ko domin zai sa kiyi arziki? "Ba zaki bauta ma Allah da kuma kudi ba". (mat 6:20).

**HADDACEWA:**

- Misalai 3:5-6 "Ka dogara ga Ubangiji da zuciya ɗaya, kada ka dogara ga abin da kake tsammani ka sani. A cikin dukan abin da kake yi, ka tuna da Ubangiji, shi kuma zai nuna maka hanyar da yake daidai".
- Zabura 32:8 "Zan koya maka hanyar da za ka bi, Zan koya maka, in kuma ba ka shawara".

**MABUDIN GASKIYA:**

Sa'anda Yesu ya kira mu mubishi, ba zamu san dukan matakai na tafiyan da ke a gaban mu ba, amma zai nuna mana mataki nag aba da zamu dauka da kuma a karshe inda zamu sauka shikenan.

**MARTANINKI:**

1. Mene kiranki a wannan lokachi na rayuwa?.
2. Menene Allah yake kiranki kiyi masa yau?.

**DON KARIN KARATUN NAZARI:**

Kira ta Os Guinness (Guinness, 2003)

Jerin Wa'azi "Me Yasa Nake Nan?" da Robert Morris

www.gatewaypeople.com

## DARASI NA 12: YIN TUNANI, YIN BUKI, KADDAMARWA.

1. **YIN TUNANI**

   Yayinda muke tunani akan wadannan darussa da muka duba a wannan takarda, wadanne abubuwa uku ne da kina fatan kada ki manta?

   a.

   b.

   c.

**2. YIN BUKI**

Yi tunani akan gudumuwan wasu a wannan taro tawurin wannan bita, kiyi binbini akan gudumuwan kowanensu a wannan bita, ki roki Allah ya baki Kalmar karfafawa ga kowannensu.

1.

2.

3.

5.

**3. KADDAMARWA**

Addu’ar kaddamarwan mu:

“Ubana na gode maka domin kofan shiga a cikin maganarka tana bada haske. Na gode maka domin kalmarka, yana da rai kuma cike da iko… Na gode maka, ubana (daka bani ruhu) na iko da kauna da kuma na natsuwa da kwanciyan hankali da horaswa da kuma kamun kai. Inada ikon ka da iyawan ka, domin ka zamnadda ni, kamar mai hidima da kuma mai bayar da sabon alkawari (na ceto tawurin Kristi).

Na manta da abubuwanda suke a baya na, ina kusa kai zuwa abububuwa da ke gabana. An giciyeni tare da Kristi, duk da haka ina rayuwa, amma bani ba, sai dai Kristi da ke rayuwa cikina, kuma rayuwan da nike yi a yanzu a jiki ina yine da bangaskiya na dan Allah, wanda ya kaunaceni ya bada ransa domina.

Yau ina saurarar maganar Allah.

Na yarda na kuma mika kai ga maganarka, ubana, maganarka ba zata rabu da ganina ba, zan ajiye su a tsakiyan zuciyana, gama rai ne a gareni, warkaswa da lafiya ga dukan jikina, na kiyaye zuciyata da dukan tsaro, gama daga cikinta ne ruwan rai ke bulbulowa.

Yau b azan bar jinkai da nasarta da gaskiya su rabu dani ba, na rataya su a wuyana, na rubuta su a allon zuciyata, domin haka zan sami tagomashi, da ganewa mai kyau da martaba a gaban Allah da mutuum. Yau jin dadi na da marmari na duka suna cikin shari'an ubangiji, kuma abisa shari'an sa ina tunani dare da rana, don haka ina kama da itacen da aka dosa abakin ruwaye, a shirye in bada iyaya a lokachina, ganyayena ba zai yi yaushi ba ko ya yankwane, kuma duk abinda nayi zanyi nasara.

Ina gode ma Allah wanda akullayaumi yana bani nasara a cikin Kristi.

A cikin sunansa nayi addu'a." (Copeland, 2005, pp. 135, 136)

NOTES

NOTES

## BIBLIOGRAPHY

Bock, D. H., George; Hendricks, Bill. (2015). Gano Baiwarku. Teburin Podcast. An dawo dagahttps://youtu.be/ frro6eLa-JY
Bower, M. (1997). Nufin jagoranci : gudanar da kasuwanci tare da hanyar sadarwar shugabanni. Boston, Mass.: Makarantar Kasuwancin Harvard. Chambers, O. (1992). Ƙarfina ga Maɗaukakinsa: ingantaccen bugu a cikin yaren yau: littafin zinariya na Oswald Chambers.
Grand Rapids, Mich.: Gano House Publishers. Collins, J. C. (2001). Yana da kyau ga girma: dalilin da yasa wasu kamfanoni ke yin tsalle-kuma wasu ba sa (eded 1st). New York, NY:
HarperBusiness.
Copeland, G. (2005). Addu'o'in da suke amfana da yawa ( 25th commemorative ed.). Tulsa, OK: Harrison House.
Covey, S. R. (1989). Halaye bakwai na mutane masu tasiri sosai:
maido da da'a. New York: Simon da Schuster.
Dawson, J. (1997). Ceto, Abin sha'awa da Cika. Seattle, WA:
YWAM Bugawa.
Fortune, D., & Fortune, K. (1987). Gano baiwar da Allah ya yi muku.
Tsohon Tappan, NJ: F.H. Revell Co.
Foster, R. J. (1988). Bikin horo : hanyar zuwa girma na ruhaniya (Rev. 1st ed.).
San Francisco: Harper & Row.
Gilbert, L. (2015). Binciken Kyaututtukan Ruhaniya Kyauta. An dawo daga https://gifts.churchgrowth.org/cgi-cg/gifts.cgi?intro=1
Greenleaf, R. (1977). Jagorancin Bawa (An cika shekara 25 ed.).
Mahwah: Paulist Press.
Guinness, O. (2003). Kira: nemo da cika maƙasudin rayuwar ku. Nashville, Tenn: W Pub. Rukuni.
Hammond, L., & Cameneti, P. (2000). Sirrin addu'a mai ƙarfi
: gano harsunan zuciya. Tulsa, Okla: Harrison House.
Hendricks, B. (2013). Menene Baiwar ku? Kyauta.
An dawo daga www.youtube.com/watch?v=sXLvI3LJHUw
Jacobsen, W. (2000). Yana so na. Tulsa, Ok: Ƙungiyar Bugawar Insight.
Kahl, J., & Donelan, T. (2004). Jagoranci daga zuciya : zabar zama shugaba bawa (ed 1st ed.). Westlake, OH: Jack Kahl da Associates.

Kise, J. A. G., Stark, D., & Hirsh, S. K. (1996). Lifekeys: gano ko wanene ku, dalilin da yasa kuke nan, abin da kuka fi kyau. Minneapolis, Minn.: Bethany House Publishers.
Koch, R. N., & Haugk, K. C. (1992). Faɗin gaskiya cikin ƙauna: yadda ake zama Kirista mai dagewa. Louis, Mo.: Stephen Ministries. Lencioni, P. (2002). Rashin aiki guda biyar na ƙungiya: tatsuniya ta jagoranci (eded1st.). San Francisco: Jossey-Bass.
Littauer, F. (1986). Bishiyar halayen ku: gano ainihin ku ta hanyar buɗe tushen. Waco, Tex.: Littattafan Kalmomi.
Maxwell, J.C. (1993). Halin nasara. Nashville, TN: T.
Nelson Publishers.
Maxwell, J.C. (2000). Kasawa gaba : juya kurakurai zuwa matakan tsakuwa don samun nasara. Nashville, TN: Thomas Nelson Publishers.
McGinnis, A. L. (1979). Dalilin abokantaka : yadda ake samun kusanci da mutanen da kuke kulawa. Minneapolis: Augsburg Pub. Gida McGinnis, A. L. (1997). Rayuwa mai daidaitawa : samun nasara a cikin aiki da ƙauna. Minneapolis: Augsburg.
Meyer, J. (1995). Filin yaƙi na hankali: yadda ake cin nasarar yaƙi a cikin zuciyar ku. Tulsa, Okla: Harrison House.
Ministoci, C. S. (1999). Littafin Aikin Taro Na Tsabtace. Takarda da aka gabatar a Taron Tsabtace, Colorado Springs, CO. www. cleansingstream.org
Muryar, B. (1999). Watsewa : Yin 'yanci cikin Kristi gaskiya ne a rayuwa. Nashville, Tenn.: Latsa LifeWay.
Muryar, B. (2004). Imani da Allah. Nashville, Tenn: Broadman & Holman.
Morgenstern, J. (2000). Gudanar da lokaci daga ciki: tsarin rashin hankali don sarrafa tsarin ku - da rayuwar ku (eded1st). New York: Henry Holt.
Morris, R. (2015). Gaskiya kyauta: karya tarkon da ke tattare da sauki. Nashville, Tennessee: Rukunin Bugawa W, tambarin Thomas Nelson.
Munger, R. B. (1992). Zuciyata--gidan Kristi: labari ga manya da matasa (Rev. ed. na biyu). Downers Grove, Rashin lafiya: InterVarsity Press.
Noland, J. R. (2015). Bayanan martaba na Personalysis. An dawo daga http://www2.personalysis.com/assessment/
Pegues, D. S. (1997). Gudanar da rikici hanyar Allah. New Kensington, PA: Gidan Whitaker.
Rahma, T. (2014). Strengthsfinder 2.0 (Bugu na Mutanen Espanya. ed.). New York: Gallup Press.
Sanda, K. (2014). Guda hudu G. Sadarwar Kirista,

Ka'idoji na asali. An dawo daga www.peacemaker.net Senge, P. M. (2006). Ilimi na biyar : fasaha da aiki na ƙungiyar ilmantarwa (Rev. and updated. ed.). New York:
Kwanan Biyu/Kudi.
Smalley, G., & Trent, J. (1986). Albarka. Nashville: T. Nelson. Smedes, L. B. (1984). Gafara kuma manta: warkar da raunin da ba mu cancanci ba (eded 1st.). San Francisco: Harper & Row.
Smith, M. (2005). Hidimar Addu'a ta Theophostic. Takarda da aka gabatar a Ma'aikatar Addu'a ta Theophostic, Babban Taro, Irving, TX. Spears, L.C. (1998). Hankali akan jagoranci: hidima, kulawa, ruhi, da jagoranci bawa-shugaba. New York: Wiley.
Swenson, R. A. & Swenson, R. A. (2002). Margin : maidowa, motsin rai, jiki, kuɗi, da tanadin lokaci ga rayuka masu yawa; Ciwon wuce gona da iri : koyon rayuwa a cikin iyakokin ku.
Colorado Springs, Kolo: NavPress.
Voskamp, A. (2010). Kyauta dubu ɗaya : kuskura don rayuwa cikakke daidai inda kuke. Grand Rapids, Mich.: Zondervan.
Wagner, C.P. (1994). Baye-bayen ku na ruhaniya za su iya taimaka wa Ikklisiya ta girma (edar cika shekaru 15). Ventura, Calif.: Littattafan Regal.
Weaver, J. (2000). Samun zuciyar Maryamu a duniyar Martha: samun kusanci da Allah cikin shagaltuwar rayuwa (1st ed.). Colorado Springs, Colo: WaterBrook Press.

ESTHER
INITIATIVE